🌓🌙BAYAN WATA🌙🌓
AFTER THE MOON🌕

BY
NARNAH KANWAR SOJA
MARUBUCIYAR
MIJIN MAGE
FARASHIN SO
BIYAYYA GA UWA
DUHU CIKIN HASKE
RUHI BIYU
HANYAR RUWA
MAI CIKI CE
MADOBIN IDO
AHLIN LASHKAR
PRINCESSS RAHILAT
RAYUWAR UMMAH
BAYAN WATA

SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

GABATARWA

Wanan  Labarin zai fara zuwa muku Ranar Litinin da yardar Allah shafin shine asalin gundarin labarin matafiya ne wanda suka bar kasar su zuwa wata ƙasa domin muradun su, a sannan labarin ne cikin labari domin dukkanin su zasu bamu labari mabanbanta daga cikin tafiyar su sanin haƙiƙanin labarin lallai sun mun shiga ciki domin karatu tare....

Masu laɓe a cikin group wanan sabon littafi ku fitoo kafin ayi waje daku fatan zaku na sharhi da share Nagode..

Chapter 1 & 2
Tafiya Mabuɗin ilimi

بسم الله الرحمن الرحيم
اللهم صل على محمد وسلم

Ƙara duba email nasa yayi nan John ya dafa kafaɗar sa " Common man muna late fa " ajiyar zuciya ya sauke mai nauyin gaske cikin tunani tsarin ɓarauniyar hanyar da zasu bi daga Kano zuwa Dubai cikin kwana 150
Addu'a suka fara bayan kammala wa motar tasu ta zubin taxi ya tashe da matuƙar gudu
Duk wani abun buƙatar su na abinci kuɗi sutura tare da abun bukatar su na yau da gobe yana cikin wannan motar
Hannu tasa tana lissafi cikin buguwar zuciya

" Kano (Nigeria) Yobe → Chad → Libya → Egypt → Israel → Jordan → Saudi Arabia → United Arab Emirates (Dubai)
Yanzu wanan ƙasasshen dukka sai mun tsallake su Innallilahi wai'na illaihin rajiuon " take hawaye ya fara zubuwa a idon ta, harara Maryam ta buga mata " Haba Ihsan meyasa kina da saurin kuka ne tafiya ce kawai duk da munsan akwai wahala a hanyar mu amman ai muna tare ke tuna buri da muke dashi a rayuwar mu idan bamubar Nigeria ba ina zake samu bukatar aikin

da muke so " ..

Tunda suke magana Yazid na latsa wayar sa wanda yake buga game nasa cikin nishadi sosai

Yazid ,
Yaro ne mai shekaru 25 a rayuwar sa  ya gama makarantar secondary school sai dai yana da Babban buri a rayuwar sa ma buɗe katafaren Company gine gine hakan yasa ya yanke shawarar zuwa ƙasar Dubai inda suka samu labarin ana zuwa neman kuɗi sosai kuma ana dace domin kuɗaɗen su mai matukar girgiza ruhin mai neman kuɗi da wanan niyyar ya baro gida

Ihsan
Yarinya ce wacce take da shekaru ashirin a rayuwar ta sai dai ta tasu daga gidan marayu na nan Kano tabbas Ihsan yarinya ce mai basira sosai ga kuma kyau da ilimi sai dai Ihsan yarinya ce mai neman na kanta duk inda taga zata samu kuɗi tana zuwa neman aiki lungu da sako Ihsan yanzu babban burin ta shine ta samu jari sosai wanda zata fara kasuwanci gari zuwa gari har ma da ƙasasshen waje Amman yanzu dole sai ta tafe Dubai domin samun aiki ko na aikatau ne domin cikkar muradun ta.....

John
Idan ana neman yaro mai karfe da fikira to John ya samu wanan shaidar babban abokin Yazid kinan wanda  suka ye makarantar tare sai dai shi ya samu aikin soja wanda aka Kore sa daga aiki dalilin mugun ƙazafin da abokan sa suka masa shi kuwa ya yanke hukuncin baren ƙasar domin ya tafe nemo kuɗi kodon huci takaice abinda aka masa .....

MARYAM
Kuna neman matsoraciyya yarinya ga tsoro ga rashin jin magana ga kuma taurin kai sai Maryam wacce take da shekaru ashirin da ɗaya chifff Maryam ta tasu gaban muguwar kishiyar uwa wacce sai abinda tace baban ta zaiyu hakan yasa take azabtar da Maryam ta kowani yanayi kyakkyawan yarinya ce ga ilimi boko da na arabiyya sanan tayi karatun health care ƙaramar nurse ce  dalilin barin ta gida kuwa kishiyar uwarta ne ta yanke mata hukuncin auren wani tsoho a unguwar sa wanda baban ta ya amince hakan yasa ta gudu tabar gidan sai gashi ta haɗu da ƙawa a titti wato Ihsan wanan yasa ta yanke shawarar binsu chan ko ita ma zata tsira da gujje gujje da take ye akan hanya ..

ADO
Engineer kinan saurayi mai shekaru ashirin da tara mai hazaƙa da basira baiye makarantar ba sabo da tsananin talauci wa da bai san uwar sa ko uban sa ba a kan titti ya gansa yana tafiya bashi da kowa ko komai Amman ko wacce mota ce ya iya gyara ta sanan ya iya duk wani abinda ya shafe igiyar wuta, sanan ya taɓa shiga ƙasar Chad neman kuɗi a takaice dai Ado yana cikin wanan sahun tafiyar domin yana da buri mai yawa a rayuwar sa ...

A haka suka kama hanyar Yobe state domin fara tafiya zuwa Chad, muna fatan tafiya yayi kyau a dawo da cikakkiyar nasara...

Please don't forget to comment and share
Continued........
Narnah ƙanwar soja ✍️✍️
—

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON

BY
NARNAH KANWAR SOJA

💫Royal Star Association,💫
SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaka gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

Page 1 & 2

Yawan sharhin ku yawan typing banyi alkawarin posting kullum ba ,
mujeee zuwa tafiya ta fara tafiya
show me some love guy's 🩷

بسم الله الرحمن الرحيم
اللهم صل على محمد وسلم

Zaman motar ya fara yi musu nauyi tun kafin su iso Yobe daga nan sai suka shiga ƙasar Chad da yamma, rana ta fara dusashewa cikin baƙin gajimare da iska mai ɗauke da ƙura gaba ɗaya zuciyar su ta fara karaya koda kuwa basu furta ba.

John ne ya fara gyara zaman sa yana duba agogon hannunsa.
"Wannan hanya wallahi kamar babu wanda ke bi ta yanzu," ya faɗa cikin ƙaramin murya
Maryam ta kama hannun Ihsan tana danne tsoro da karfin hali, "Mun riga mun fito, ai sai gaba."

Motar ta dinga kutsawa cikin kura da kankara, har aka kusa tsallaka wata ƙaramar kwazazzaba da aka samu a tsakiyar duwatsu. wani ƙara mai firgita ya tashi daga motar.
"Grrrrkkk—krrr!"

Kafin su fahimta, tayar gaba ta tsinke da wani ƙarfi motar ta faɗi gefe  kamar zata tintsire Yazid ya damƙe sitiyari yana ƙoƙarin tsayar da ita amma komai ya gagara Ado ya rike bangon motar yana fadin:
"ALLAHU AKBAR!"

Sai kawai suka ji "dduuummm!", motar ta buge da wata babbar dutse, ta tsaya cak  anan ne shiru ya biyo baya, babu motsi, sai sheshshekar Ihsan da Maryam suna kuka.

Yazid ya fito daga motar yana duba tayoyi, idanuwansa sun cika da 'kura. "tayar gaba da gefe

duk sun ƙone  clutch ɗin ma ya tarwatse. muna cikin matsala mun rasa motar mu."

John ya farka daga karyewar da ya sha, ya dubi hanya yana shan iska mai zafi, sannan yace: "Wannan ba hanya ba ce, wannan tabo ne. mu kwashe kayanmu mu shiga cikin dajin nan idan muka tsaya nan dare zai riske mu, barayi ko dabbobi za su iya far wa."

Babu wanda ya musa kowa ya ɗauki nashi kaya cikin tsoro da damuwa. Ihsan na riƙe da kwalbar ruwa, Maryam na lulluɓe da veil tana kare jikinta daga cizo.sun fara takawa cikin ƙaton daji, cike da raɗaɗin ƙasa mai kaifi da ciyayi masu yankan ƙafa  Ado na gaba yana amfani da torchlight wayarsa yana duba hanyar da zasu bi tsakar dare ne lokacin da suka hango wani tsohon baranda kamar dafa-gari. ba za a iya ce masa gida ba, amma yana da rufi da bango.

"Mu tsaya nan mu huta. Allah ya kawo safiya lafiya," Yazid ya faɗa.
Maryam ta kifa kanta a kafadar Ihsan, tana kuka cikin salo mai ciwo, "Idan na mutu a hanya ki ba baba sanina... ki ce Maryam ba ta jure tsanani ba." John ya dan murmusa cikin firgici, "Zamu mutu fa kafin mu isa Dubai idan muke tsoron hanya haka tun a Chad."a haka dare ya cigaba da raguwa, zafin rana ya mayar da dare sanyi mai shigowa jiki kowa ya kwanta da kaya a jikinsa yana jiran asuba da fata, da addu'a, da fargaba.

Dare ya yi tsayin gaske kamar zai hana wayewar gari ,sanyi ya ratsa kowane sassa na jikinsu, kowane yana neman ɗan nutsuwa da kwanciyar hankali, amma babu shi.
sai dai ƙasa mai kaifi da raɗaɗin tunani.

Asuba na ƙaratowa, Ado ya farkar da su ɗaya bayan ɗaya.
"Ku tashi, lokaci yayi... sai mu yi sallah kafin rana ta fito."

Sun fito daga barandar ruwan zufa da ƙura na hade da jikinsu. kowa ya shimfiɗa ɗan zane a ƙasa, suka gabatar da sallah da natsuwa da ƙasƙantar da kai. bayan sun idar, Yazid ya zaro ɗan kwali daga cikin jakarsa.

"Ga ruwa nan da snacks ɗin biscuit da gurasa. Amma sai mu kiyaye amfani da su, ba mu san inda zamu isa da kafafu ba."

Ihsan ta amsa kwalbar ruwa tana goge fuskarta da tissue, Maryam na gefenta, kukan jiya ya bar wani ɗan kumburi a idonta.

"Da gaske zamu ci gaba da tafiya ne?" Ta faɗa da rauni.
"Me kike tunani?" John ya juyo yana gyara jakarta. "Za mu jira motar da ba za ta zo ba? Ko barayi su zo su kwashe mu da kaya?"
hka suka kammala shiryawa, suka kwashe komai da suka iya dauka akwai leda mai ɗauke da tuwo da miya wanda suka saya kafin shiga Chad, ruwan robobi guda shida, da wasu kuɗaɗen kasar da suka musanya kafin barin Nigeria.

Ado ya latsa map ɗin da ya saukar a waya, duk da babu signal sosai, yana ƙoƙarin duba hanya mafi kusa da wata rijiya ko gari “wannan hanyar zata kaisu cikin wata ciyawa mai tsayi—amma akwai wata ma'boyar ruwa da nake tunawa da ita daga lokacin da na taba zuwa Chad.”sai suka kama hanya, dajin yana cike da tsuntsaye masu shewa, ƙasasshiyar ƙasa na sa ƙafafunsu zubar da gajiya. Ciyayi na yanka ƙafafun su, ganyaye na goce su a fuska.

Yazid ya riƙe jakar abinci yana gaba, John na gefe yana duba kowane motsi, kamar soja na sahun fama. Maryam na tsakiyar Ihsan da Ado, amma ita ce ta fi fitar da kuka.

"Gsky, idan Dubai ne zai kashe mu haka, to wallahi zan koma gida."
"To sai a auri tsoho, ko?" Ihsan ta harare ta cikin dariya mai taɓarɓarewa.
Maryam ta kyalkyale da dariya cikin hawaye" ke Ihsan wallahi da aure Baba audu gwanda na mutu a hanyar nan"

Sun dauki kusan awa biyu suna tafiya cikin daji kafin suka kai ga wani tabo mai ɗan sanyi, kamar ruwan fanfo ya ƙyalƙyala sama, suka zauna a can suka sha ruwa suka ci ɗan abu.
Yazid ya duba agogon sa. "Zamu ci gaba da tafiya bayan minti talatin... don kada rana ta fara zafi mu gaji."

Cikin wannan rana, sun fara fahimtar cewa tafiyar nan ba zango ba ce, ba yawon shaƙatawa ba ce hanya ce ta ƙalubale da jarumta, da fahimtar juna. Kuma suna cikin ita....

Garin da suka zauna sun ɗan ji sanyi da natsuwa bai kai awa biyu ba, sai ga wani ƙara ya karad'e sararin samaniya. wani irin hadari ne ke tasowa daga gabashin jeji, ganye na yaye

sama, ciyayi na karyewa, iska na tashi da kura mai kauri "Na shiga uku! wannan fa kamar guguwar jeji ce!" Ado ya faɗa yana rintse ido "Ku tattara kayan nan! Ku kamo jakunkunan ku!" Yazid ya ɗaga murya.

Cikin daƙilewar lokaci suka fara tattare kayan su, Maryam ta faɗi jakar ruwa, sai kuma aka jiyo busa kamar karar motar iska tana fashewa wata bishiya ta karye tana gangarowa da sauri! John ya ɗago Maryam da sauri suka fice daga wajen,kowa ya rikice.ƙasa ta ɗan girgiza, sai ƙara da kuma wata shanya mai ɗauke da ganye da ƙasa ta tashi ta rufe hanya.

"Wayyo Allah na! kayi mana sauƙi!" Ihsan ta yi ihu.

Kowa da nashi, sai suka gudu sun rarrabu kadan, amma a ƙarshe suka taru bayan sun kusan rasa juna. tafe suke da keɓaɓɓen numfashi, zuciya cike da tsoro da gajiya, bayan tafiya mai nisa da hawan ƙasa da tsallake kwari, sai suka hangi wani ƙauye a can gefe da daji. wurin tamkar ya zauna a gaban dutse ne, akwai ɗan ruwa yana kwarara daga wani ƙanƙanin dutse.

Ado ya saki numfashi. "Wannan tamkar lahira muka tsira daga ciki muka dawo duniya ne wallahi."Yazid ya yi dariya. "Kai dai karka fara wahalar da mu da falsafa yanzu shin ka taɓa zuwa lahira ne."
Ihsan ta tura masa kafa, "Wai yanzu ni dai idan na nitsu zan rubutta wanan hargitsen cikin wannan littafin domin tarihi sai na rubuta wani Irin Jeji da na shiga."suka tafi da dariya, duk da gajiya ta cika jiki.

Sun isa ƙauyen, mutanen gari suka karɓe su da jinkai, suna ba su ruwa da wuri su huta. Sun zauna suka ci abu kaɗan, suka kwanta ƙarƙashin inuwa, Ihsan na kwance a gefe ta ce, "Wallahi idan na isa Dubai, zan fara kasuwancin ganyen magarya na gaji da dogon buri."dariyar su tashi, kowa ya ƙwalla dariya mai sa hawayen idanu.

Bayan hutu da shan ruwa, suka sake tashi da niyyar cigaba da tafiya gobe da safe. kamar ba suba, suna dariya, suna kwance da juna kamar ƴan uwa, daga cikin hargitsi da wahala, nishad'i ya fara zame musu masoyi.

Kwanaki sun shige suna lissafa wa cikin jeji da ƙasa marar alamar birni, bayan haɗari da suka fuskanta, motar su ta hantsila a ƙasar Jamhuriyar Chad, suka kasa gyara ta, sai suka bar ta can da ƙyallen tarihi suka fara tafe da ƙafa, kamar masu hijira daga duniya zuwa mafarki.tun daga lokacin ne suka soma 'kulla wani ɗaurewa da ba wai jinƙai kaɗai ba, amma kamar ana zuba

wani zuma a zukatansu, suka zama kamar ƴan uwa da aka haifa daga ciki guda.

Maryam, mai natsuwa da laushin murya, ita ce jinyar jikin su duk sanda ciwon tafiya ya kama daya, za ta tsaya ta fidda ƙananan kayan asibiti daga cikin jakar matafiyar ta—ta fiddo da tawul, ta sha da ruwa, ta gyara bandage. Ita ce ta fi sanin yadda ake shafe jiki da ganyen da suka ci karo da shi a hanya domin rage raɗaɗi.

Ihsan kuwa ta fara zama ƙawarta ta gaskiya. su biyu idan suka haɗu sai dariya da tsokana, suna ƙoƙarin mantar da sauran wahala. Ihsan da bakinta mai ɗaukar dariya, ita ce ke ba su nishadi, tare da Yazid wanda kullum da sabuwar waka a bakinsa. Yazid na iya busa leda da furar baki har kowa ya manta da gajiyar tafiya.

John, babban mutumin da ke ɗauke da baƙin laya a wuyansa, shi ke gaba da su a koda yaushe ƙarfin jikinsa da jajircewarsa ke kare su daga tsoron jeji da dabbobi. Idan dare ya fado, John ne ke ɗebo itace, yana hura wuta, yana saka su su ji kamar gida suke ciki.

Ado, ƙwararren masanin hanya, shi ke tsara hanya. Duk sanda suka tsaya yana fiddo taswira ko yana duba taurari da rana don sanin gabas da yamma,baya cika surutu, amma idan ya buɗe baki, kalmarsa zata zama haske.

A daren da abinci ya ƙare, sukayi shiru gaba ɗaya. ba kowa da bakin magana sai ƙarar cikin da ke ɗaukar wululu. Maryam ta rufe idonta da ƙirjinta, tana share hawayen da ba kowa ya gani ba. zai dai Ihsan ta ɗan matsa kusa da Yazid, suka fara raira waka:

"A cikin duhu akwai fata,
A cikin yunwa akwai madara,
Rana ta fito daga bayan wata..."

John ya sa dariya, ya ce:
"Kun sani, idan muka tsira daga wannan tafiyar, zaku fi daraja fiye da zinariya a gare ni."

Ado ya duba sama, yana murmushi da ƙyamshi, sannan ya ce:
"Idan muka kai Libya lafiya, zan gaya muku sirrin da ya sa na bar gida."

John ya ɗago kansa, ya ce:
"To, mu haɗa zuciyarmu." suka kama tare da muryar da ke daɗi ga kunne, duk da gajiya da yunwa, suka rera:

Bayan wata akwai dare,
Bayan dare akwai haske,
Bayan yunwa akwai cika,
Bayan hawaye akwai dariya.

Idan rana ta ɓuya,
Mun san wata zai leƙo,
Idan hanya ta dushe,
Mun san ƙafafunmu zasu kai.

Bamu daina ba, bamu ja baya ba,
Zamu cigaba har gobe ta zo.
Mu da juna, zuciya ɗaya,
Rana ta fito daga bayan wata"…

Yayinda suka rufe baitin ƙarshe, wutar da John ya kunna ta ƙara walƙiya, kamar yadda wata ke ɗaukaka cikin dare.

Tun daga wannan daren, wannan waƙa ta zama taken tafiyarsu duk sanda sun gaji, ko dare ya musu tsayi, ko cikin su ya fara kuka, sai daya daga cikinsu ya fara:

> “Bayan wata…”
sauran su kuwa sai su ɗaga murya cikin amsa, kamar ruwa da tsuntsu:
“…akwai dare… bayan dare akwai haske…”
suna shiga cikin sabuwar rana da sabuwar fata.

continued..... narnah ƙanwar soja ✍

💫Royal Star Association,💫

https://chat.whatsapp.com/DoFR3n8ILtI1RB5Zd2z2IT

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON
BY
NARNAH KANWAR SOJA

💫Royal Star Association,💫

SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

Page 3 & 4
28 / 4/ 2025
Yawan sharhin ku yawan typing banyi alkawarin posting kullum ba ,
mujeee zuwa tafiya ta fara tafiya
show me some love guy's 🩷

بسم الله الرحمن الرحيم
اللهم صل على محمد وسلم

Wurin da suka iso na kusa da bodar Libya da Niger wata ƙaramar unguwa ce dake shan gajiyar gabar duniya motar da ta biyo hanya daga Agadez zuwa kusa da Libya ta sauke su a unguwar Sakar, inda suka ce daga nan za a wuce da ƙafa har zuwa Sabha a cikin Sahara.

Yayinda dare ke neman yin nisa, suka haɗu da wasu 'yan tsirarun matafiya da suka ce akwai hanya ta gefen jeji wacce ake bi don gudun jami'an tsaro.

John ya ja su a gaba, yana ɗauke da wata ƙaramin ƙaho na ruwa da bag ɗin burodi guda ɗaya kacal. Yazid da Ihsan na bayansa suna rera wasu baitin Bayan Wata da karfin zuciya, yayinda Maryam ke sanye da hijabi mai kauri, tana riƙe da Ado a hannu, suna tafiya a hankali cikin

duhun dare.

Amma a kwana na biyar  a cikin Sahara, bayan sun wuce wani yashi mai launin toka, a lokacin da rana ke ƙoƙarin ɓullo daga gabas,
Maryam ta hantsila ƙasa da karfi, “Aaaaaaah…!” ta fasa ƙara, jikinta na karkarwa kamar daji na girgiza, gaba ɗaya suka tsaya cak.
Ihsan ta durƙusa da sauri, tana girgiza ta. “Maryam! me ya faru?”

Maryam ta duba ƙafarta—tsohuwar alƙalamin takalmi ya tsinke, kuma dutsen da ta taka ya huda tafin ƙafarta, jini na zuba kamar famfo.

Sai hawaye suka cika idon Ihsan
Ado kuwa ya durƙusa yana duba ciwon da kwarewa kamar ƙwararren likita  “Dole ne mu tsaya nan  ba za ta iya cigaba da tafiya ba ” ya faɗa don yagaji da dogon tafiyar da babo matsaya,

John ya kalli yamma, inda duhun jeji da yashi ke cike da sauti marar ƙauna. “ba mu da lokaci… idan muka tsaya, mayakan macijin nan zasu iso.”
“mayakan macijin?” Ihsan ta tambaya da fargaba,
“'Yan fashin daji Idan suka same mu, ba abinci ba ruwa ba 'yanci...” ya dakata yana ɗauke numfashi
Yazid ya ɗago kai, idanunsa na cike da yaji  ya ce:
 “To a ɗauketa  ba zamu tafi mu bar Maryam ba !” yana kauda fuska don dai har ga Allah cikin wanan yunwar bashi da kuzarir ɗaukar ta ,sai John ya ce da karfi “Ni zan ɗauketa!”

Bai jira amsa ba, ya ɗauki Maryam sama kamar jaririya, jikinta yana rawa saboda zafi da ciwon da ke yawo cikin jinin jikinta suka cigaba da tafiya , duhu ya koma, rana ta sake bayyana da ƙyalli, amma zuciyarsu na makare da tsoro da azaba.

Lokacin da rana ta ɗora bisa tsakiyar sararin sama, Ado ya sha ruwan ƙarshe da suka rage ya yayyafa kan Maryam.

Yazid kuwa ya saka dariya duk da gajiya yana cewa “Yau rana na cin mutum, amma jiki na cin

gado…" sai Ihsan ta hau waka a hankali:
"Bayan wata… akwai dare…"
John ya karɓa cikin murya mai ƙarfi kamar jarumi
"Bayan dare… akwai haske…"

Suka kama waƙar cikin kuka da dariya a lokaci guda waƙar ta zama mafakar zuciya.

Maryam da aka daura a bayan John, tana raɗa wa kanta:
"Zan rayu… saboda ku…"

Washe gari rana na haskakawa cikin yashi kamar zinariya, suka iso wata ƙaramar sansanin 'yan gudun hijira da ke bakin Libya, wanda wasu likitoci daga ƙungiyoyin jinkai ke taimaka wa nan ne aka kwantar da Maryam cikin wani tantin asibiti na wucin gadi An gyara ciwonta da tsafta, aka bata allurai da ruwa, har ta fara murmushi.

John da Ado suka sauke ajiyar zuciya. Yazid kuwa ya durƙusa ya shafa gashinta yana cewa: a cikin kunnen ta "kin tsira Maryam… ki tabbata za ki rayu har mu ga Dubai!"

Ihsan kuwa, da ta zauna a jikin wata tsohuwar matashiya mai suna Mama Simbi—wacce itama gudun hijira ce daga Ghana ta kalli sauran matafiya da kuma wasu daga cikin mutanen sansani, sai ta ce da natsuwa:

"Kafin rana ta sauka yau… zan ba ku wani labari. Labari ne wanda ban taɓa fitar da shi ba… kuma shine zuciyata ke ɓoyewa tun ina zan bayyana labarin da Narnah ƙanwar soja ke da burrin fitarwa sai dai bata samu dama ba ne Ihsan zanyi amfani da wannan damar."

Gaba ɗaya suka zauna, wasu suka ɗebo ruwa, wasu kuma suka jera kan buhuna da katifu. cikin nutsuwa da natsuwa, Ihsan ta gyara zama, idonta na kallon nesa kamar tana komawa

zamanin da ya wuce.

Sauran matafiya suka runtuma cikin nishadi, wasu suna cewa, “Labarin fa kenan!” wasu na gyara zama kamar za su rubuta da likitochin da tawagar Bayan wata duk suna sauraron ta

(Yanzu fa lokaci yayi na shigowar sabuwar rayuwa cikin Bayan Wata—wannan labarin Ihsan da za ta fara ba su a sansani, zai kasance labari cikin labari, wanda zai haɗa ƙauna, yaƙi, al’amuran fada da sirrin da ta ɓoye har yau. )

PRINCESS RAHILA
EPISODE ONE
2000 Years Back

Sunanta Rahila – kyakykyawa ce tamkar hasken wata, bakar fata mai sheƙi, jikinta dirin coca-cola shape gashinta ya sha bamban da na kowa a masarautar Buga African, kuma idanunta sun yi farin haske har cikin duhu. murmushinta na bayyana haƙora masu tsabta da kyau halittarta ta ban mamaki ce, fiye da na kowace mace a wannan ƙarni.

Rahila ita ce tilon 'yar da King Numan ke da ita bayan shekara da shekaru ba tare da samun ƙarin 'ya'ya ba, sai ya tara soyayya da dukiyarsa gaba ɗaya ya miƙa mata. Baiwar da bai ba kowa ba, ya ba Princess Rahila – wacce ake kira da wannan suna cikin girmamawa.

Masarautar Buga African ta kasu gida biyar:

1. Yankin Burum

2. Yankin Dusrum

3. Yankin Tursum

4. Yankin Kurum

5. Babban yanki – Buga African, karkashin King Numan.

Tunda mahaifiyarta ta rasu tana da shekara biyar, Rahila ta tashi tare da mahaifinta  duk wata buƙatarta ana cikawa, kuma soyayya ce ke ratsa tsakaninsu tana da shekaru goma sha biyar amma ta riga ta kware wajen amfani da makamai kamar takobi, kwari da baka, guggar zana da salon yaki – duk sabili da Slave Kodo, babban gwarzon bawa kuma mai ba King Numan kariya.

Fadar King Numan cike take da dukiyar duniya da bayi duk da cewa bai ƙara aure ba bayan rasuwar matar sa, yana amfani da wannan damar wajen tilasta wa matan bayi duk matar bawa da ta rasa mijinta, ko baiwar da take kyakkyawa, za ta faɗa hannun sa.

Rahila ta kai shekaru ashirin kyaunta ta kai kololuwa duk sarakuna da attajirai sun so mallake ta amma ta ƙi. a cewarta, ba za ta bar fadar mahaifinta ba kuma ba za ta zauna ƙarƙashin kowane namiji ba. Wannan ra'ayi nata yasa wasu sarakuna suka rasa idanuwansu saboda kallonta da soyayya.

Ta yi imani cewa mahaifinta zai rayu har abada ta ɗauka rayuwarta zata kasance cikakkiya har abada a haka ne ta fara koyon mugunta, ta nuna ƙarfin hali da alfahari. Ta san ta fi kowa kyau da ƙarfi. Ta ƙi yarda wani namiji ya kwanta da ita.

Tana ganin ƙarfinta da na mahaifinta da na mayaƙa – musamman Slave Kodo – zai iya kareta har abada amma sai wani abin mamaki ya faru…

Lokacin da ta dawo daga kogin da ta saba wanka, tana kwance a gadonta, bayi biyu na tausa ƙafarta, wasu na shiryata, sai wani bawa ya shigo cikin gaggawa tayi mamakin ganin shi ya shigo ɗakin ta ba tare da izini ba. Cikin fushi ta watsa masa mari har sai da ya firgita.

Yana kokarin cewa “The king sees…” amma ta katse shi da bacin rai, “So what? He's my father, I can go to him anytime I want!”

Da ƙyar ya fice, amma cikin mintuna sai ga King Numan da kansa ya shigo ɗakin wani abu ya dame shi, hakan yasa Rahila ta shiga fargaba – abu da ba ta taɓa ji ba. Bai taɓa shigowa ɗakin ta ba da kansa.

"My baby, we must leave Buga African immediately!" ya faɗa cikin damuwa.

"What? Leave our kingdom? What is happening?” Rahila ta tambaya, cikin tsoro da rashin yarda.

"Zuma people (Dursum) have invaded our palace! We've been betrayed. Even our soldiers have been sold out!" in ji King Numan.

"NO, Father!" ta ce cikin jin kai. “nu shugabanni ne! Dole mu yaƙi mu mallaki su mu mayar da su bayi!”

Ta ɗauko takobinta mai haske, wanda ta keɓe, tana shirin yaƙi. Amma fa, yaƙin da ya zo ba kamar sauran bane.

Cikin hanzari, Slave Kodo ya shigo. “Your majesty! Prince Tarhim na Dursum ya shiga tsakiyar fadar da mayaƙansa!”

King Numan ya kama hannun Princess Rahila. "My jewel, please, follow Kodo. He will take you to safety."

“No! I won’t run like a coward!” Ta ce cikin kuka da bacin rai.

Amma King Numan yasan lokaci ya kure  kuma burinsa shine ya ceci tilon 'yarsa
King Numan ya dube ta da ido mai cike da ƙauna da alhini. Hannunsa yana rawa yana riƙe hannun 'yarsa Rahila, kamar yana ƙoƙarin ƙara ji da ƙarfi a jikinsa da ya fara rauni.

"My jewel... I know my time has come," ya furta cikin rauni. "But I will not let them take you. You must live, even if I die."
Princess Rahila ta dafa ƙirjinsa da duka hannayenta biyu, idonta na cike da hawaye masu ƙyalli, tana girgiza kai. "No Baba, don’t say that! You will live! we will fight together!"
Amma Sarki Numan ya girgiza kansa cikin sanyi."I’ve seen this in my dream... Kodo knows what to do. He’s been waiting for this day."

Yayi kallon ƙarshe ga Slave Kodo, wanda yanzu ya yi shiri da kayan yaƙi, gashi yana kama da jarumin da ba a taɓa ganin irinsa ba.
"Kodo," in ji Sarki Numan cikin murya mai ƙarfi, "take her... and make sure she survives. That’s an order."
Kodo ya durƙusa, ya ce da kwarjini:By the gods of Buga Afirican, I will protect her with my life."
Princess Rahila ta sake fashewa da kuka. Tana janye hannunta daga na mahaifinta tana cewa:"Baba... don’t let them take our land..."
Sarki Numan ya matsa kusa da ita, ya sa hannu a bayanta ya rungume ta na ƙarshe. Ya furta a kunne ta da ƙasa sosai:
"You are the land now. You are Buga Afirican. Go... before it’s too late."
Sai ga wata ƙara ta fashe daga wajen fadar. Wuta ta fara tashi daga ɓangarorin fada, ƙamshin hayaki da jini na ratsa iska. Wakilan Zuma da Prince Tarhim sun karya ƙofa, sun shigo da mayaƙa cikin izza da azama.
Slave Kodo ya ɗauki Rahila kamar jaririya, ya fice ta wata ɓoyayyar ƙofa dake bayan gadonta—ƙofar da aka gina shekaru dari da suka gabata domin irin wannan lokaci.
Sarki Numan ya tsaya da kafarsa, ya zare takobinsa mai daraja, wanda aka gada tun zamanin kakanninsa Ya fuskanci mayaƙan Zuma da ƙarfi, yana ba da na ƙarshe na jinin sarauta domin kare masarautarsa.

An bar fadar cikin hayaki. An bar sarki cikin yaƙi. an fita da Rahila cikin duhu.

Wannan rana ce ta zame wa Buga Afirican tarihi Ranar da wata sarauniya mai ƙarfi ta rasa gida, ta rasa uba, amma ta samu sabuwar rayuwa—rayuwar da zata yi nasara ko ta mutu tana ƙoƙari......

Continued by narnah ƙanwar soja ✍️

https://chat.whatsapp.com/DoFR3n8ILtI1RB5Zd2z2IT

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON

BY
NARNAH KANWAR SOJA
( Sayeddan Addah )

💫Royal Star Association,💫
SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

Page 5 & 6

Yawan sharhin ku yawan typing banyi alkawarin posting kullum ba ,
mujeee zuwa tafiya ta fara tafiya
show me some love guy's 🩷

بسم الله الرحمن الرحيم
اللهم صل على محمد وسلم

Haka abin ya faru da Sarki Numan haba ɗaya mutanensa sun gaji da mulkinsa, wasu daga cikin

mayaƙansa sun juya masa baya, suka sayar da kansu ga mutanen Dursum, wanda suka sayi rabin mayaƙan domin samun nasara a kansa.

"Kado,  ka kula da ‘yata. Ita kaɗai ce abin da na mallaka," inji Sarki Numan, ya faɗa wannan karo fiye da goma.

"Eh, mai martaba, zan kareta da raina," Kado ya sake amsawa cikin nutsuwa.

" Baba ka bar ni na tafi tare da kai!" Princess Rahila ta faɗa cikin kuka, tana faɗawa jikin mahaifinta.

Ba ta son wani abu ya same shi  ita fa ba komai ba ce idan ba tare da mahaifinta ba.

“Je Kaɗo , tafi yanzu da ‘yar gadona. Ka kiyaye ta kamar zinariya.” Sarki Numan ya faɗa da murya mai ƙarfi, irin ta jarumai, sannan ya juyawa wajen baya yana barin gurin.

Princess Rahila ta sake gudowa ta rungume mahaifinta daga baya da jin ɗumin hawayenta a bayansa, zuciyarsa ta raunana sai dai ya ƙi juyawa saboda kar ta hango hawaye a idanunsa — alamar rauni ga jarumi kamar shi.

Duk da haka, yana son Rahila ta ci gaba da tunawa da shi a matsayin jarumin sarki, gwarzon da yaƙi bai faye shi ba, ba mai zubar da hawaye saboda galaba ba.

Bayan wani lokaci, Rahila ta saki mahaifinta, sannan ya tafi ba tare da ya waiwayo ba.
Baba Baba  Ka kalleni ko sau ɗaya,” Rahila ta faɗa tana fāɗowa kan gwiwowinta, amma Sarki Numan bai waiwaya ba yana ƙoƙarin ɓoye hawayensa.“My princess, dole mu tafi yanzu,” Kado ya faɗa yana ƙoƙarin tashi da ita, amma ta ture shi.“Kar ka kuskura ka saka kazamin yatsunka a kaina!” ta faɗa cikin ƙiyayya.
(Duk da girman haɗari, girman kai na sarauta ya mamaye ta.)
Kado bai ce uffan ba. ya saba da halayenta, tun da shi ya horar da ita duk da haka, shi kansa bai tsira ba suka fice ta wata sirriyar hanya da ba kowa ke san da ita ba, sai dai shi da Sarki Numan.
Yayinda Sarki Numan ya dawo fadar sa, sai ya tarar da rabin masarautar an lalata ta. Mayaƙan Dursum sun riga sun mamaye wajen.
Sarki Numan ya shiga ɗakin sirrin da ke ajiyar makamai, ya sa tufafin yaƙi, ya ɗauki manyan

takubba guda biyu zuciyarsa cike da fushin jarumi, ya kuduri niyyar mutuwa a matsayin gwarzon sarki maimakon guduwa kamar gwanin fargaba.

A lokacin yaƙi...

Yaƙin ya riga ya barke, sara suka hannu da ƙafa. Sarki Numan ya fafata kamar zaki, yana yanke mayaƙa tamkar bishiyoyi lokacin da ya hango Prince Dursum, tun da farko ya ɗauka Prince Tarhim ne, sai dai da ya kalli fuskar, ya gane cewa uban ne — Sarki Mujus. Da haka ya soki kansa ƙasa, alamar ƙarshen nasarar da yaƙin zai iya kawo masa.

Sarki Numan ya ci gaba da gwabzawa har sai da zuciyarsa ta fara kasa dukan da kyau. Bugun zuciya ya rikice, zuciyarsa ta mutu da ganin 'yarsa cikin halin ƙaskanci ya sulale ya fāɗi ƙasa, ya zubar da makamai, hawaye na zuba daga idanunsa.

“Ba zai yiwu ba! wannan ba gaskiya ba ce!” ya ƙwala ihu cikin azaba.

“…  ku bar ta ku kyaleta, ku bar ta haka kawai,” Sarki Numan ya roƙa yayin da aka jawo Princess Rahila cikin sarka, tana kuka.

Jikinsa ya kasa tsayawa, ya durƙusa, yana kallon Prince Tarhim yana ja da sarkar Rahila, har ta durƙusa ƙasa yana kai ta gaban mahaifinta, yayin da wasu zaratan mayaƙa suka kewaye su yanda yake ganin ‘yarsa tamkar bayi, ya girgiza zuciyarsa sosai.

Princess Rahila ba komai ce a wannan lokaci ba face bawa, jikinta da datti da ƙura, gashinta ya bazu.

“Ga ‘yarka, Sarki Numan babu sauran princess, yanzu bayi ce a ƙarƙashin masarautar Zuma,” inji Prince Tarhim, ɗan Sarki Mujus — jarumin da ya kashe dabbobi da suka kai hari garinsu, Zuma shekaru 27 ya fafata yaƙe-yaƙe masu yawa.

Dogo ne, baƙi fari, da kyakkyawar fuska. Fuskarsa da sunansa suna tayar da hankali, musamman ga mata.“Wannan ba zai faru ba!” Sarki Numan ya ƙara faɗa.

“, ku bar mahaifina shi ne Sarki na Buga Afirka,” Rahila ta faɗa cikin kuka.
Sarki Mujus ya fusata, ya jawo gashin kanta. Rahila ta yi ihu cikin ciwo da azaba.
“Great king kike kira? kin san abin da mahaifinki ya aikata wa mutanen masarautata?” inji Mujus.
Sarki Numan ya ce, “Kaɗo ne ya yi alkawarin kare ki.”
“Baba Kaɗo ne ya ci amanar mu,” Rahila ta faɗa cikin murya mai cike da raɗaɗi. Mahaifinta ya firgita.

“Kado? Amintaccena?”
“Eh, Baba ya ƙaddamar da komai.”
Kado ya bayyana yana faɗi, “Na tuna kuka na iyayena da ‘yar’uwata lokacin da suka mutu a hannunka. kayi musu hukunci da wuta saboda haraji na jure, na koya darasin rayuwa har na zama bawan da kake amincewa da shi amma yau sai na ɗauki fansa ta, in ga yadda ‘yarka ke zama bayi, kamar yadda ka mayar da ‘yan’uwanmu bayi.”Sarki Numan ya ƙara fashewa da kuka, “Kado, me nayi maka har ka yi haka?”
“Zan bar ka da rai, Sarki Numan amma zan tabbatar ka gani da idonka lokacin da ‘yarka ta fuskanci cin mutunci kamar yadda wasu suka fuskanta.”
“Don Ubangiji… a kyale ta ku daina wannan,” Sarki Numan ya ce yana ihu, yana ƙoƙarin miƙewa a lokacin ya sharɓi wuka daga hannun wani mayaƙi.
...ya sharɓi wuka daga hannun wani mayaƙi, ya sharɓa a cikinsa da ƙarfi, jini ya fara malala daga bakinsa, yana kallon ‘yarsa da ƙyalli na ƙarshe a idanunsa.
“Rahila…” ya furta cikin muryar da ta dushe.
“Babaaaa” ta ƙwala ihu da karfi, tana ƙoƙarin tashi daga kan guiwowinta, amma ankai mata dukan da ta sume nan take.
Kafin idon  Sarki Numan ya fadi ƙasa shikake, ya rasa numfashi daga nan, aka ɗaukaka tutar Zuma a saman fadar Buga Afirka aka kama bayi da mata da yara, aka raba su. Masarautar Buga Afirka ta fadi ƙasa, ta koma cikin tarihin da ake karantawa da ba’a taɓa tsammani ba.

"Father please don't dîe. Please don't... don't, I beg you! Somebody please help me. Please save my father." Princess Rahila tana roƙon mayaƙansu

"Save your... breath.. my jewel, take...take...care of yourself. I love you my baby rahila ke tuna ke sarauniya ce juye duk abinda kekeso da zaran kin samu dama " King Numan aya faɗa wanan shine sautin sa na ƙarshe ,

"Father please, please stay with me please don't leave me." p rincess Rahila  ta faɗa cikin ƙunar zuciya tana daman jan tokobin daga cikin sa sai da tasha wuya kasancewar hannunta da Chain

"Father please don't leave me.
"Father no...you can't do this to me, you can't leave me here all alone!" Princess Rahila ta f ad'a da ƙarfi wanda gabaɗaya ta razana gun da ihun ta  ta ɗaga tokobin sama tana kallon yanda jinin mahaifin ta yaki wanzu akai , ta saita dai dai  cikin ta da wuƙar ,

"let me go you  ....Let me go right now, ka bani tokobi na zan kashe kaina na huta  Princess Rahila  ta faɗa tana ihu lokacin da Prince Tarhim ya ƙwace makamin hannun ta ,

"Tarhim ka barta ta mutu  duk da haka uban ta baya nan da zaiga kalan hukunci da zan mata let her kill her safe and go ,  Shashasan ya kashe kansa already don haka ita ma barta ta kashi kankara kowa ya huta useless girl I do not care anymore"

."Father, do you think it will be okay for us da zamuga tana kashe kanta " ya tambaya ciki da sonjin amsa daga mahaifin nasa" ƙwarai da gaske wannan shine tabbatar da cewa mun gama samun nasara a wannan yaƙin....

"Keep quiet, shut up you  son of bitch , don't talk to my father like that!" Prince Tarhim ya faɗa yana tunkuɗe ta daga kusa dashi

Wanan yayi dai dai da zartar War tokobin king Mujse saitin kanta sanadin bangaja da ta sama tayi ƙasa tokobin ta kwace wa kanta
cikin haushe da takaice rashin samun ta raised up his sword again after yayi rashi nasara daga farko da zumar filli kanta charraf Prince Tarhim ya kama hanun sa kafin tokobi sa yakai head of princess Rahila " father u don't have to do this akaiw hanyoyi da dama da zamuyi amfani akanta

"What is wrong with you son?  shin kaman ta yanda Uban ta ya kashe ɗan uwan ka ?" king Mujse ya faɗa cikin kaɗuwa da mararrin jiki .

The king Mujse  Taki yaji komai ya zama sabo burin sa kawai kashe ta ko zai rufe wanan chapter daya jima yana mafarkin samun nasara akan sa.
Prince Bella firstboy na king Mujse wanda ya bashi matsayi prince yana da mata Princess Afrah wanda suki zauna lafiya sun haifi yarinya ɗaya Aflim tana da wata biyar Prince Bella ya haɗu da mummunar ƙaddarar sa da ta janyo baƙin cikin da tsananin ɗaukar fansa na king Mujse..

King Mujse ya aika  Prince Bella zuwa meeting to wanda za'ayi a birnin Kursum inda manya manyan sarakai zasu haɗu su tattauna to solve a issues affecting their kingdom prince  Bella Jauro got dressed and said goodbye to his family. inda suka rabo d kyar ta hanyar kukan baby Aflim king Mujse ya amsheta da rarrashin ta yana cewa shi bazai samu zuwa ba duk da cewa yaron sa yana. tareda da sabon baby babu but ya hallarchi taron kasancewar shine next of the king .

Shin a hakane zaka jagoranci kujerar mulki idan bana nan ? zaka ajiye duty saboda  akan kukan baby ?!  a lokacin da ya hangi tsantsan tausayi baby Aflim da mutuwar jikin Prince Bella ,

"Her mother is here and your mother is here too. We are all here to take care of her so please, you must leave at once son." King Mujse ya maimaita maganar cikin ƙwarin guiwa da yaki bawa Prince Bella ,They didn't know that it was the last hug and last goodbye.

Duk sarakuna sun kammala haɗuwa a inda Aki jiran king Numan wanda ya ƙaraso da dukkan tawagarsa cikin isa da mulki da kaddara dukkan su suka miƙi tsaye wasunsu har ɓoya bayan wasunsu suki , kasancewar sa Jarumin jarumai da babo mai ƙarfin ikon sa a wannan nahiyar ,
Duk abinda yake faruwa Prince Billa  ya chigaba da zama ba tareda ko kallon sa yayi ba
In one-time ba zato ba tsammani ya zaro tokobin sa ya sara kansa taki y rabi gida biyu sai jini da ya wantsala umarni ya bawa Slave's nasa da susa kansa cikin akushi su ƙona ganganr jikin sa da wuta a idon duniya su

" ku ɗauki tokan ganganr jikin sa kukai ga uban sa ku sanar masa dukkan abinda yafaru ya sanarwa ɗaya daga cikin dakarun da suka sa prince Bella rakiya inda yayi arrest na sauran suka zama Slave's nasa .

A lokacin da King Mujse yaji wanan Labarin sosai ya razana inda queen Afra ta. kamu da heart Attack a wanan time Prince Tarhim ya chigaba dajan ragamar shugabancin Dursum

After sometime soon king Mujse ya warke yafara plan tareda mutanen sa plan to their revenge hakan ya faru sukayi nasara ganin ga king Numan kwance a cikin jini a masaurautar sa king Mujse yana shirrin Kashi Princess Rahila prince Tarhim ya dakatar dashi .....

BACK TO STORY
"Father, wanan shegiyar yarinyar can't dîe just like that. I have a better plan for her ." Prince Tarhim ciki da tsananin fushi da fusata King Mujse baxai iya jira ba yaji wanan plan nin ba King Numan already dead but still bazai iya yafe mishi akan kashe ɗan sa ba dole sai ya kashe ta zai samu sallama He would do anything to complete his revenge mîssion
"Father, you will be helping her if you kîll her now. a rashin sani uban ta ya tsira daga punishment za muka shirya masa taya zamu barta itama jikinta ya tafe a banza Rahila dole ta biya bashin da ubanta yaci akanmu mu barta har sai ta roqe mutuwa da kanta da muguwar azabar dazamu ɗanɗana mata let's kill her slowly

Kanta ta ɗaga sama tana kallon sa da idannunta da suki wanzuwar da jini a kowani tsako daki da jijjiya a. ƙwayar idon "son of bithch kill me now you have only one change kar kabari wanan damar ta wucce ka Tarhim because jaine mutum na farko da zan fara kashewa idan ka barni a raye da Rayuwa ta
"I shall kîll you all one by one. gabaɗaya ku sai kun ɗanɗane zumar kaɗai na mutuwar ku a tafkin hannuna i sweer with my beloved father ." "I, the princess of Buga Afirican promise you all today. sai na kawo ƙarshen ƙasar Dursum ta durgusa a kan guiwarta sai na sa kun tsani kanku ta faɗa with her fire eye's bata damu da zaratan mazajen da suki kewaye da ita ba burinta kawai suyi zuciya su kashe ta ko zata huta da wanan bak'ar rana da ko. mafarki batayi tunanin kasancewar sa ba ..

"Son, did you hear that? jinin Numan yana kewaye da ita she is devil too kill her rayuwarta tamkar na uban ta ne" , dogon tsaki yaja Prince Tarhim ya kasa fahimtar meyasa ta kasance very hot stubborn duk da cewa tana ganin tana daga da mutuwa even in the face of dànger.
"Father, I know how to handle people like her."
"One day, you will beg for my mercy." Prince Tarhim ya faɗa yana matso da hannun sa akan

fuskar ta matsar da fuskar ta tayi da tofa masayawun da ya haɗa jini in his face dariya ya kicce dashi yawa hannu ya gogge yana dungule hannu yakai mata wani mugun nashi da saida ya fasa mata kefin bakin ta

King Mujes daya amince da yaron sa ya yanke hukuncin ya barta ta kasance matsayin baiwar su ,it felt like a dream to Rahila batasan da cewa watarana wanda yaki chan sama duk matsayin da mulkin sa ko ƙaddara sa da dukiyarsa watarana zai faɗo ƙasa warwas ba kaman ƙitfawar ido

King Mujse later cût off king's Numan head from his body. ya ƙona ganganr jikin sanan ya umurce dukan bayin sa suyi wasan harbil harbil da kansa a sansanin masarautar buga Afirican the most powerful king of Buga Afirican bazai iya aikata komai ba kasancewar yau da kansa ki wasa a sansanin masarautar da idon dubanne mutane da bai ɗauki su a bakin komai ba yaki wulakanta su sa kiran su baye marasa amfani sai gashi shine yau a wannan matakin
All that happened front of Princess rahila wacce taki kuka ta tana rogon sa da yadaina azabtar da kan mahaifin ta sai dai kash hakan ƙarawa king Mujse ƙarfin guiwa yakiye da azama

Har abada zaki yafi ƙarfin ayi wasa a gaban shi har akai masa raini ko suka sai dai idan ya kasance mattace har yaro zai iya matsowa don yayi wasa dashi hakan ta kasance kansa ya zama abin nunawa da dariya ga muradun buga Afirican .

Cikin Chain a maƙale da wuya ta da hannun ta da ƙafarta Prince Tarhim yana kan dokin sa yana janta cikin ƙunchi suka kama hanyar Dursum ana ball da kan mahaifin ta wanan abin yafi mata muni akan yanda mutanen buga Afirican suki kallon ta a wulaƙanchi even when she asked water sai dai tasha ruwan hawaye ta wanda suki zuba layi layi tsananin tsana da ɓaci rai da mugunta daban daban taki saƙawa prince Tarhim tabbas indai ta ƙungiya shine mutum na farko da zata kai lahira kasancewar bata da wani babban maƙiyi sama dashi ......

Princess Rahila batayi tsammanin isowar Dursum zai kasance sillar tsayawar hawayen ta sakamakon ganin cincirindon al'ummar garin sun fito kansu da ƙwarƙwartansu suna watsa mata duwatsu wasu kuma tumatur da takalma lallai ta sami tarbar na musamman haushi mulkin ubanta da nata taki amsar hukuncin daga gari su

Numfashi ta ne ya tsaya chakk lokacin da aka harba wani talkami ya sauka akan fuskar ta tunawa da cewa idan ace yau yana raye babo wanda ya isa ya ɗaga mata ɗan yatsa a gaban ta Taki ta yanke jiki sunammaya inda yayi dai dai da isowar su wani bakin ɗaki su dark and hurt prince Tarhim ya tsuma ta da umarnin kawo ruwan mai ɗumi aka watsa mata taki ta dawo daga suma ta cikin. azaba ta ƙwala ƙara tunda taki for the first time taga irrin wannan duhu duk da cewa takan iya azabtar dawasu  a irrin sa batayi tunanin kasancewar haka a garita ba .

NARNAH KANWAR SOJA 🖊️💞💝💝

https://chat.whatsapp.com/DoFR3n8lLtI1RB5Zd2z2IT

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON

BY
NARNAH KANWAR SOJA
( Sayeddan Addah )

💫Royal Star Association,💫
SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

Yawan sharhin ku yawan typing banyi alkawarin posting kullum ba ,
mujeee zuwa tafiya ta fara tafiya
show me some love guy's 🩷

بسم الله الرحمن الرحيم
اللهم صل على محمد وسلم

Cikin shigar dogon riga irrin nasu aka gyara mata gashin kanta tari da sa mata ado akan gashin ta a hankali taki taka ƙasa cikin ƙasaitacciyar takunta na sarauta Princess Afrah kinan tsohuwar matar Prince Bella tsaya tayi da miƙa hannu a gun amintacciyar baiwarta Adila amsar akushin tayi wanda ta haɗa girke na musamman sai ƙamshi takiye a hankali ta tura ƙofar d'akin nasa wanda aka hada masa komai da komai na kayan al'adu na sarauta hango sa tayi ya fito wanka ya ɗaura wane yafi a kungumin da cikkar halittar jikinsa ya bayyana taki tsikar jikinta ya tashi tabbas tasan Prince Tarhim yafi tsohon mijinta ɗan uwa sa komai da komai a jikin sa taki wane sha'awar ta ya motsa na son kasancewa dashi a gado ɗaya tun baya chan tanason Prince Tarhim just pretending takiye domin manya sun shiga tsakiyar auren ta da Prince Bella, chunkusa fuskar sa yayi ganin yanda ta shigo masa ɗaki kai tsaye ba sanarwar ko Slave Harun baigayamasa yana da tabbacin ta masa abu ne ko tahanasa gayyamai tana zuwa ganin haka .

Princess Afrah ta ajiye abin hanun ta jikin ta har yakiye burinta kawai ta rungume sa ko zata samu sassauci a hankali ta matso kusa da jikin sa tana harhaɗa ƙafa sakamakon baƙon yanayi da taki riskinta kanta ciki  da sauri ya katse ta da nuna mata hannu " Please don't do it what do you want from me? me yasa zakishiaga ɗakina with no exuceses "

" You know I love him yes I love him but know he is no more he gone what can I do Prince Tarhim kai kawai nakigani na tuna da ɗan uwa ka kasani yanzu inason ka fiyyeda rayuwar ta i love you now and forever please am begging you please love me nasan "..

Numfashi sa ne ya tsaya chakk ya daina sauraren kowane maganar da taki furstawa daga ƙaramin bakin ta ya za'ayi

"It was no secret that his brother loved  Afrah  so much when he was alive  sanan yanzu kuma ta ina zata ce tana sonshi how can she can sleep with the former wife of his blood brother like how ya za'ayi nayi making love da matar yaya na no respect for the dèad at all."

"Afrah , can you please excuse me? I need to rest, I just got back." He said,  trying to send her away in his room  ,"I can help you rest my love, you can place your head on my laps and I shall stroke your hair while you sleep

" Afrah I want to be left alone,. Thank you. so much"

"I can't leave you alone my love, not when we are going to be one very soon." Afrah tana faɗa ta turesa unexpected suka zube a ƙasaitacciyar shimfiɗ'a gadon sa tana kallon ƙwayar. ido. sa da ta kwanta akan budaɗiyar ƙirjin sa yana ƙoƙari tureta gaba-daya ta saukar mai da wane azazzababbin kasala da yaki dakon sa tsawon shekaru masu yawa domin shi bai kasance mai kwanciya da mata na masarauta ba

Da sauri Slave Harun ya faɗo cikin ɗakin cikin tashin hankali da rashin ganin hanya da galibi ganin abinda yayi karo dashi Princess Afrah akan Prince Tarhim cikin good moment
da sauri ta miƙi ko kallon sa batayiba ta wucce domin yanayin ta ya canza fiye da tsammanin burinta kawai taki ta kwanta ka zasamu realife.. juyuwa taye ko mai tatuna Slave Harun ta ka'la cikin sauyin fuska tace

"Where is your manners? How could you just run into the prince's chamber like that? I will dèal with you later, now just leave this place at once, as you can see, the prince is busy with his woman!" Afrah tafaɗa cikin burin kunya da fushi
"I am sorry my princess, I am sorry my prince, but this can't wait. The princess of Buga Afirican Princess Rahila has escaped from captivity!"  Slave Harun ya sanar musu yana ƙoƙari juyawa da sauri Prince Tarhim ya sauko cikin hanzarin tunowa da kalmar ta na karshe

"You will be the first person I will kîll if I get the chance. "What? How... how did ...how did that happen?" Prince Tarhim ya faɗa yana zaro tokobin sa yasha ɗamara

"Ehm...ehm... My prince, muma kanmu bamu lura ba kuma muna wanan gun a a a a a

"You were what? Can't you talk? You even called her a princess. How could you! How could you call a prîsoner a princess, ehn? are you màd?" Princess Afrah shouted at the Slave
A dàngerous girl like Rahila escaped and all princess Afra  ta damu da har yanzu suna kirar ta da sunan ta maimakon ta tuna cewar Rayuwar su tana cikin hatsari da rashin tsaro

."I said it! I said it! We should have just kîlled that daughter of a mónster back there but Tarhim didn't listen to me, now see, she has escaped!

"ya akaye haka ya faru ?  ya zaku gayyamin kuna busy celebrating and you forgot your duty. murnar gidan ubanwa zakuyi ohhhhh shittt "  King Mujse ya fad'a a harzuƙe ya miki tamkar Tsohon Zaki aiki ya Kuma close all the way's find her now isaod now

"Th.at girl is going to be more dàngerous than her father. How could she have escaped with her hands and feet tied with a chain, how?"

Sorry my king  Prince Tarhim yace mu  cire mata chain a dark room tell us to yana nagana sai ga Prince Tarhim ya shigo da ƙanƙancewar idon sa da suka sauya ya danne fusatar sa domin bada haƙuri ga king yasan tabbas yanzu baida wanda yakinin haushe sama dashi mussaman a wanan lokachin

"I am very sorry father, please forgive me. Let me go and look for her, I am sure she hasn't gone too far." Prince Tarhim ya faɗa yana ƙara ladabtar da kansa ƙasa ga idon mahaifinsa daya zama tamkar garwashi wuta , "How can you even think of going out there to look for her? Have you forgotten Kaine na farko da zata fara kashewa a cikin Zafaffan kalaman ta sanan a wane dalili dazaka ce wa bayi su kumceta daga Chain don kaga ta shiga dark room mafi hatsarin d'akin horo am already lost my  first son I won't take any chances with my  second son."

"Baba kana tantama akan jarumta ta ?  na kashe sadaukai dewa a baya nayi yaƙi sosai neme gwarzon mayaƙi dabbobi nine sarkin mafarauta daji ka amince dani i will go and find her  I promise you I will back with her "

"No son, you don't understand,  She can be more dàngerous than any a animals." bai kamalla maganar sa ba sukafara sar'kewa numfashi da tari wane gurd ne yashigo my king hayaki ne ya turnike daga bayan mu idan ka bamu izzine zamu iya zuwa dubawa

Prince Tarhim ya xabura yaga  direction daga inda wutan ke tashi saman dokin sa .
Sarki yabi ɗansa  tare da wasu Slave's da suki gaba da bayan su
Prince Tarhim yayi mamakin ganin fillin ajiye dabbobi su ya kama da wuta wasu na mutuwa wasu kuma sai gudu sukiye gaba-daya kukan su yana karaɗe fillin a taki a ka fara watsa musu ruwa da ƙasa ta ko'ina

Tana maƙale a saman ittace tana kallon yanda suke ƙoƙarin kashe wutar  dabbobin su na mutuwa ɗaya bayan ɗaya hakan yasa ta fara ajiyar zuciya da cewa " kafin ku fara mutuwa yana da kyau kuga mutuwar dabbobi ku , baxan taɓa yafe muku ba never".

Kune sillar  mutuwar mahaifin na kune sillar wargaza masarautar ta kune sillar azabtar da ne and you will see what happened to you all a sannu a hankali

Bayan wani lokaci kadan ta farara kuka duk da cewa abataso hakan ba tanason kasancewa vrave and strong women Nan tafara tunanin ta hanyar da zatayi escaping ta Kuma buga Afirka tunuwa da babo wane abu mai amfani a wanan masarautar a gunta yasa ta tuni da fansar ta kafin tayi tunanin barin Dursum place

Princess Rahila a hankali ta sauka a saman Bishiya  ganin duk hankalin su bakan arzikin dabbobi su ta chigaba tafiya chan ta shiga daji nan ta hango wane bush da sauri ta shiga ba tare da tunanin ko a kwai wane abuba tunanin ta ya tsaya na matafiya ne shiga tayi burinta ta samu relief tayi bachi ga dan banzan yunwa da kishin ruwa da tsinci kanta a cikin muguwar wanan yanayin ganyen bishiya tagani a dai dai tun da yasa ce babban bishiya hawa tayi ta tsinki ganyen ta zauna taci sa tsaff tana zubar da hawaye Zafaffa shiga cikin bush nin taye numfashi sama sama , taki  dutse biyu ta dauka da idea ya zumata sakamako duhu da ya ƙauraye dajin a taki wuta ya kama tsa a kan chiyawa da tara gaban ta ta kwanta cikin minti kaɗan wahalalen bachi yayi gaba da ruhin ta

Princess Rahila tana cikin bachinta mai tsananin bakin ciki da wahala a hankali tafara jin wane sanyin abu yana ratsa ƙafarta na haqqu mai laushi lumshe idon ta tayi tunuwa da yanayin masarautar ta idan ana mata tausa cin wane azazzababbin ciwon ne yasa ta razana ta farka a harzuƙe tana ƙwala ihu da sauri ta Toshi bakin ta domin kar Dursum people suji wanan sautin na ta a  dukkan dajin ...........

Muna haɗa turanci da Hausa a labarin Princeces Rahila kuyi haƙuri laifin Ihsan ne amman zata gayamanna dalilin ta nayin hakan
ku chigaba da kasance wa a littafin bayan wata labarin matafiya guda biyar wanda zasu bamu labarai mabanbanta......

To be continued…

https://chat.whatsapp.com/DoFR3n8lLtI1RB5Zd2z2IT

BY
NARNAH KANWAR SOJA
( Sayeddan Addah )

💫Royal Star Association,💫
SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaka gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

Page 9 / 10

Yawan sharhin ku yawan typing banyi alkawarin posting kullum ba ,
mujeee zuwa tafiya ta fara tafiya
show me some love guy's 🩷

بسم الله الرحمن الرحيم
اللهم صل على محمد وسلم

Ta yi saurin janye ƙafarta daga macijin da ya naɗe a jikinta, amma abin ya riga ya faru macijin ya cije ta nan take lokacin da ta motsa, sannan ya ɓace cikin daji kamar bai taɓa zuwa ba , Rahila ta yanke gefen rigarta ta kuma ɗaure ƙafarta don hana venom ɗin macijin yaɗuwa daga wurin da ya shafa
ta buƙaci taimako cikin gaggawa, amma su waye za su taimaka mata?

A lokacin da mutanen Zuma suka kashe wutar da ke ƙasar gonar sarki, wasu daga cikin dabbobin sun riga sun ƙone har lahira, wasu kuma sun ƙone sosai amma sun tsira.

Sarkin Mujsee ya ji zafi sosai saboda gonar dabbobin na ɗaya daga cikin manyan hanyoyin samun kuɗi na sarki.
mutanen da ke daga sauran masarautu suna zuwa masarautar Zuma don siyan madara saboda yawan shanun da sarki ke da su a gonar, amma yanzu, mafi yawan shanun sun ƙone a wutar.

Tashin dakararru da ƙashin dabbobi daga cikin gonar yana zama taki ga gonakin noma a masarautar Zuma, kuma sarkin yana tunanin me zai faru da amfanin gonar su wannan shekarar.
Akwai sauran gonaki a masarautar Zuma, amma wutar ta shafa mafi girman gona a masarautar. Sarkin ya kalli cikin zuciya, yana ɗaukar dabbobin da aka ƙona suna fita daga gonar

"King , ina ganin kana buƙatar hutu na tabbata komai zai tafi daidai  za mu samu wasu dabbobi nan ba da jimawa ba." Yaron sarki, Mujse yayii ƙoƙarin kwantar da hankalin mahaifinsa.

"Yaro na, ya kamata ka gano gaskiyar abin da ya faru a gare ni ya kamata ka gano wanda ya ƙona gonar nan."

"Na tabbata wani ne ya aikata wannan ta yaya gonar zata fara ƙonawa haka ba tare da wani ya yi ba? wannan bai taɓa faruwa ba, ko kuma masarautata tana cikin wani ɓoyayyen hari?" sarki

ya tambaya cikin damuwa.

"King , masarautar ba ta cikin hari mun yi nasara kan wani sarki mai hatsarin gaske kamar sarkin Numan , na tabbata sarkuna daga sauran masarautu za su ji tsoron tunanin fara yaki tsakanin masarautar mu da nasu, " Yaron Prince Tarhim  ya ƙoƙarin kwantar da hankalin mahaifinsa.

"Shin ina cikin damuwa fiye da kima? ta yaya wutar ta tashi idan ba wani ba ne da ya ƙone ta?muna cikin daminar ruwa kuma ganyayyaki da ganyen itatuwa suna sabo, ta yaya?" Sarki Mujse ya tambaya sannan ya tsaya na ɗan lokaci.
"Tarhim." ya kira bayan ɗan lokaci.
"Eh, Uba." yaron sarki ya amsa.
"Shin kana da tabbacin cewa wannan 'yar Numan tana ɓoye a wani wuri?" Sarki ya tambaya, yana duba ko ina, sai yaron sarki ya haɗa ido da shi.

Yaron sarki, Mujse ya kasance yana tunanin abin da mahaifinsa ya faɗa tun da ya ga gonar tana ƙonawa.
ya san yadda hankalin irin waɗannan mutane kamar Rahila ke aiki, kuma yana da tabbacin cewa tana can tana jiran lokaci ta sake kai hari, amma ba zai bar ta ta sake ba.

"King , kada ka damu game da wannan  zan gano inda take ɓoye, kaɗai ka yi amana da ni." yaron sarki, Mujse ya yi wa mahaifinsa alkawarin.

"Ka zama mai hankali, yaro ka rufe kofa da tagogin ɗakinka kafin ka tafi gado a yau da dare wannan yarinyar tana da hatsari.
zamu tafi neman ta gobe kuma zamu kashe ta idan muka same ta." Sarki Mujse ya faɗi kafin ya tafi gado cikin damuwa a wannan daren.

Yaron sarki Mujse da sauran su ma sun tafi bacci, amma lokacin da yaron sarki ya shiga ɗakin sa, bai samu bacci ba. ya ƙara juyawa yana cikin gajiya.

Ta yaya zai iya samun bacci alhali wanda ya yi alƙawarin kawo ƙarshen rayuwarsa yana ta faɗa?

Lokacin da ya yi tunani da kyau, ya yanke shawarar fita neman Princess Rahila a wannan

daren, bayan duk da haka yana zuwa farauta da dare a wasu lokuta.

Yaron sarki Mujse da wasu daga cikin gungun masu tsaron sa sun tafi neman Princess Rahila a cikin dare, suna shirye-shiryen duk abin da zai iya faruwa.sun ɗauki takobinsu, igiyar harba da arc, da sandar mai wuta a ƙarshen sa.

Ba su yi nisa ba kafin su sami wani daga cikin dajin yana kwance a cikin rashin lafiya.
Lokacin da suka kusanci, sai suka gane cewa wanda ke kwance a ƙasa ba wani ba ne face Warrior Princess Rahila.

Princess Rahila ta yi tunanin za ta iya yaƙi da venom ɗin macijin ta hanyar ɗaure wani yadi a ƙafarta, amma ta yi kuskure.
Bayan wani lokaci, venom ɗin ya tashi daga ƙafar da aka shafa kuma ya fara yawo a jikin ta gaba ɗaya.

Ta yi ƙoƙarin yakar ta, amma nan ba da jimawa ba ta fara jin gajiya, jikinta ya ƙasa aiki kuma ta rasa sanin kanta.
haka ta kasance a kan wannan wuri har yaron sarki Mujse da masu tsaron sa suka same ta.

Zuciyar Tarhim ta buga da ƙarfi lokacin da ya ga Princess Rahila tana kwance a ƙasa cikin rashin lafiya, ya yi sauri ya karkatar da hannunsa don jin ɗokin sa.
Ya gano cewa tana gajarta sosai lokacin da ya ji bugun zuciyarta, amma maimakon jin daɗi, ya kasance cikin ruɗani.

"Yaron sarki, mu cēke ƙashin ƙafarta mu kai wa sarki." ɗaya daga cikin masu tsaron ya ba da shawara lokacin da ya yi kamar ba ya san abin da zai yi.
"Mu ƙone ta a cikin wuta." wani mai tsaron ya ba da shawara.
dukkanin masu tsaron sun bayar da shawarwarin su, amma yaron sarki ya zaɓi bin shawarar farko bayan tunani mai tsawo.

Mahaifinsa zai yi farin ciki idan ya kai kanta ga sarki.
ba zai rasa hakan ba, ba a lokacin da Princess Rahila ta ba su komai sai matsala ba.

Wataƙila wannan zai zama abu mai kyau. wataƙila zai samu bacci cikin kwanciyar hankali idan princess Rahila ta mutu ya yi tunani yayin da ya ɗaga takobinsa cikin sarari, yana shirye ya

aikata!
"Prince Tarhim lafiya lau?" Daya daga cikin masu tsaron ya tambaya lokacin da  Prince ya dauki dogon lokaci ba tare da sauke takobinsa ba prince Tarhim ya riƙe takobinsa saman don yanke kai Princess Rahila, amma don wasu dalilai da ba a san su ba, bai iya sauke shi ba.

Eh, ta ba su wahala sosai ta yi masa faɗa mai tsanani a cikin ramin ƙasa, amma tana faɗa ne kawai don ceton ranta.
Ba ya tabbatar da ko ta ƙona gonar su, amma ko ta yi haka, rayuwarta ta cancanci fiye da dubban dabbobi. Prince Tarhim ya ƙirƙiri hujjoji da yawa a zuciyarsa game da Princess Rahila, sannan ya tuna cewa ta yi masa alƙawarin kashe shi idan ta samu damar yin hakan.

To, zai tunkari wannan lokacin idan ya iso, amma kawai ba zai iya kashe ta ba.

Ya sauke takobinsa a hankali yayin da masu tsaron sa suka kalli shi cikin mamaki.

Sun kasance cikin shauƙi na ganin Princess Rahila ta ƙare, amma yaron sarki ba ya nuna yana niyyar kashe princess a kowanne lokaci kuma ba za su iya yin komai ba saboda shi ne shugabansu.

"Prince Tarhim, sarki ba zai ji daɗi ba idan ba mu... kashe... ta ba." ɗaya daga cikin masu tsaron ya faɗi cikin ƙyama.
Prince Tarhim ya yi watsi da mai tsaron yayin da ya yi ƙasa da kyau don duba Princess Rahila.

Ya yi tunani kan abin da ya faru da ita. ya san ta a matsayin mai ƙwazo, don haka duk abin da ya sa ta zama rashin lafiya dole ne ya zama abu mai tsanani.

Ba ya buƙatar duba sosai kafin ya ga ƙafarta da ke kumbura wanda aka ɗaure
ba ya buƙatar mai fada masa abin da ya faru
daga yanayin ƙafarta ta, ya san cewa an cije ta da maciji mai guba kuma tana buƙatar magani cikin gaggawa ko kuma za ta mutu.
Prince Tarhim ya ɗauki Princess Rahila a hannayensa kuma ya nufi wajen daji cikin sauri yadda zai iya, masu tsaron sa sun bi shi cikin shiru, suna mamakin wannan juyin halin.

Sun yi tunanin inda yaron sarki zai kai Princess Rahila shin yana shirye ya miƙa ta ga mahaifinsa ya yi da ita yadda zai so?

masu tsaron suna da tambayoyi da dama a zuciyarsu yayin da suke tafiya a cikin masarauta, suna bi ta wajen daji, suna biin Prince Tarhim wanda ya riƙe Princess Rahila a hannayensa. Yaron sarki ya kai Rahila zuwa ga mai magani mafi ƙarfi a masarautar Zuma.

Ba ya san dalilin da ya sa ya yi hakan, duk da haka, bai iya kallon ta ta mutu, bayan haka ba ita ce ta kashe ɗan uwansa ba.
uban tane yayi hakan kuma hakan ya isa.

continued by narnah ƙanwar soja ✍✍

https://chat.whatsapp.com/DoFR3n8ILtI1RB5Zd2z2IT

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON

BY
NARNAH KANWAR SOJA
( Sayeddan Addah )

💫Royal Star Association,💫
SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

Yawan sharhin ku yawan typing banyi alkawarin posting kullum ba ,
mujeee zuwa tafiya ta fara tafiya
show me some love guy's 🩷

بسم الله الرحمن الرحيم
اللهم صل على محمد وسلم

Sarkin ya umarci sojojinsa su buga ƙofar mai magani yayin da ya kwantar da sarauniya Rahila a ƙasa da hankali,

Sojojin sun yi jinkiri, amma daga bisani sun buga ƙofar, sai mai maganin ta fito bayan ta tambayi wasu tambayoyi.
ta saba da mutane da ke kawo marasa lafiya zuwa gonarta a dare, don haka ba sabon abu ba ne a gare ta.

"Prince Tarhim shin ka tabbata da wannan? Mahaifinka sarki yana iya rashin jin daɗi da hakan, " mai maganin ta ce yayin da take duban  Rahila
Ta taba ganinta a lokacin da Prince ya jagoranci ta cikin sarautar su cikin ƙafa, kuma ta fara mamakin dalilin da yasa Prince ke ceton ta yanzu.

"Ni ne zan damu da hakan ke ceto rayuwarta kawai." Prince ya ƙi jin damuwarta.
"Zai yi Prince guba ta ratsa jikin ta gaba ɗaya." mai maganin ta ce "za ki iya ƙoƙarin, taimaka mata."  ya matsa, mai maganin ta fara maganin sarauniya Rahila nan take.

"idan Atishawa tayi bayan ta sha warin wannan maganin da zan kawo, to tabbas za ta tsira, amma idan ba ta yi ba, to ina baƙin ciki, babu abin da zan iya yi, ya Prince" mai maganin ta ce.

"To, sai ke ci gaba." yace ya amince.

Sojojin sun fara magana cikin husɓa suna kallon wannan abin da ke faruwa.
Prince ya koya musu cewa ba su da jin kai ga abokan gaba, kuma yanzu yana aikata abin da ya ke gargadi akai mai maganin ta tafi cikin ƙaramin gida na ta sannan ta dawo da wani haɗin ganyayyaki a cikin ƙaramin kwararan kwano.

da ta kawo warin kusa da hanci sarauniya Rahila, ta atisaye sau da dama amma idanuwanta sun kasance rufe.

"Yarinyar tana da ƙarfin zuciya." mai maganin tsohuwa ta ce, tana girgiza kai kamar tana gano wani sabon abu.

Gaskiya ta gano wani abu sabo saboda babu wanda ya taɓa samun damar atisaya bayan sun sha wannan maganin a irin wannan yanayi.

Ba kawai mai maganin ba ce, amma tana da baiwar ganin gaba, kuma ta iya gano cewa matar da take gaban ta ba ta cikin kowane irin yanayi na al'ada ba.

"Ya Prince za ka iya komawa gida yanzu, zan kula da ita. zai yi kyau." mai maganin ta tabbatar maii

Ya yi tunanin dalilin da yasa har yanzu tana cikin wannan yanayi duk da atisayar, amma mai maganin ta tabbatar masa cewa komai zai tafi daidai kuma ya yarda da ita.

Matar tsohuwa ta kasance mai taimako sosai ga mutanen Zuma, har ta kasance daya daga cikin masu maganin da suka kula da mahaifinsa, don haka me zai hana?

"Ba za ki taɓa faɗa wa kowa ba, har ma mahaifina, abin da ya faru a daren nan. sanan inason ke ɓoye ta zuwa lokacin da zan dawo bayan tafiya tafiya ta ," ya gargadi sojojin sa yayin da suka tafi gida sojojin sun amince da cewa ba za su ce komai ba ga kowa, amma ba abu mai ɗorewa ne ɓoyewa ba. da Prince Tarhim ya dawo gida, wasu tambayoyi sun ci gaba da gudu a cikin zuciyarsa.

me yasa ya ceci sarauniya Rahila kuma me zai faɗa wa mahaifinsa? Wane tabbaci yana da cewa sarauniya ba za ta kashe shi ba idan ta warke?......

BAYAN WANI LOKACI

Rana na shirin faɗuwa lokacin da Prince Tarhim ya dawo fadar fuskar sa cike da shakku da

ɓoyayyen tausayi yana sane da cewa idan aka gano cewa ya ceci Rahila, matsayinsa na ɗa ga sarki Mujse zai shiga haɗari, amma zuciyarsa ta yi shiru a kan komai – ya fi yarda da abin da yake ji fiye da hukunci ko hukuma.

A ɓangaren mahaifinsa, Sarki Mujse  ana ta cigiyar ɗansa. hana mamakin dalilin da yasa bai dawo da wuri ba, amma yana zargin akwai wani abu da ɗan nasa ke ɓoye masa.

A cikin wani ƙaramin ɗaki a ƙasan ƙaton gida mai dakuna ashirin da huɗu, tsohuwar mai magani ta shimfiɗa Rahila akan shimfiɗa mai ƙyalli da ɗan kamshi na turare, tana jin jikin nata yana murmurewa, amma zuciyarta ba ta fahimtar inda take ba.

“Ki kwanta, ki huta. rayuwa tana juyawa,” in ji mai magani cikin murya mai laushi kamar ta uwa.

Prince Tarhim, ɗan sarki Mujse , ya dawo daga tafiyarsa ta tsawon wata uku a ƙasar Habasha inda ya je neman dabarun mulki da ilimin soji. Kyakkyawan saurayi ne, mai hikima da nutsuwa, amma ba ya shiga cikin al'amuran soyayya ko fadace-fadace na fada.

Da isowarsa, ya tarar da wata ƙatuwar shiru a fada  an ɓoye masa komai, amma ba don haka ba sai da hankalinsa ya kai ga jin cewa akwai wani abu mai ɓoye a gidan sarki.

A daren da ya dawo, ya shaida ganin wani bawa yana shiga ɗakin sirri da kwanon abinci. yayi mamaki, domin wannan ɗakin ba a yawan amfani da shi sai da wani sirri mai girma.

"Waye a ɗakin?" ya tambayi bawansa.
“mai martaba ne ya hana kowa magana akai, ranka ya daɗe,” bawan ya ce da kansa yana rawa
Tarhim ya gyara tsayuwarsa, ya ce cikin natsuwa: “Na isa in sani. gobe da asuba, zan je kaina.”

Washegari da safe, Prince Tarhim ya leƙa ɗakin sirri. kafin ya buɗe, ya tsaya yana sauraron wani motsi.
daga ciki, ya ji murya mai rauni tana karanta addu’a cikin sanyin murya.
ya bude ƙofar da hankali... idanuwansa suka sauka a kan Rahila, wacce ta zauna cikin tabarma, tana daure da farin zani, gashinta ya bazu kan kafadarta.

Lokaci ya tsaya.

Rahila ta dago ido lkacin da ta kalli Tarhim, zuciyarta ta ɗan tsinke – ba domin tsoro ba, amma domin tunanin irrin halarci da ya mata na ceto rayuwar ta duk taye sanyi tasha tambaya kanta cewa me yasa har yanzu bai dawo garita ba har sarki Mujse ya gano inda take ya rufe ta yana azabtar da ita bisa laifin mahaifinnta duk gaba da faɗa da take tunkaho dashi tun da Prince Tarhim ya ceto ranta ta rasa dalilin faɗan da zataye akansa tabbas tana da. burin kashe su dukkan su to amma akan wani dalili tabbas mahaifin ta mugun sarki ne akan bayin sa ya aikata zunubi daban daban amman hakan ba wai ya na nufin a ɗauke fansa akan ta ba ita ma bawai tayi ta faɗa har tsawon rayuwar ta ba Amman rashin ganin Prince Tarhim ya tabbatar mata da tazama losser !..

Bai ce mata komai ba ya juya zuwa fada kai tsaye domin ganawar sa. da mahaifinsa Sarki Mujse ya  tsaya gaban sa  da ƙarfi da girmamawa " Ya kai baba na nasan rashin ɗa akwai cutarwa musamman idan ya kasance maƙiyanka ne sukaye galaba akanka" yakai Baba na Sarki Numan mutum ne azzalumi da duniyar mu ta sanshi akan mulkin sa baya barin kowa cikin sallama a haka muka samu nasarar shiga har fadar sa mukaye galaba akan sa shin Baba kasan dalili !?
Saboda karshen zalunci sa a hannun mu yake kuma karshen mulkin sa ya ƙare a dalilin mu mun raunata sa mun kashe sa har abada bazai dawo ba mun ɗauke fansar kashe mana namu da yayi ,to shine me laifin me yasa muma yanzu muka dawo azzalumai irinsa ka tuna mulkin da kakiye cikin aminci da adalci ya za'a yi mu azabtar da Rahila bisa laifin uban ta ?,
shin ta kashe mu ko ta dauke fansa ko ta cutar damu a'a Baba to me yasa ka rufe ta kake azabtar da ita tsawon wanan lokacin "?.

Rungumar juna sukaye nan Sarki ya share hawayen sa da cewa " tabbas na aika ta kuskure mai girma na azabtar da wanda bashi da laifi kuma nasan cewa   soyayya mai girma ce a zuciya ka daga lokacin da kaganta shiyasa na fara gaba da ita don inason ka kasance da Afra matsayin mijin ta Amman nayi laife ka gafarta min yaro na ka zaɓi muradin ka a rayuwar nan sanan sanyi murabus zaka kuma kan sarauta nan da wata ukku za'a yi wanan bukin ...

BAYAN WATA UKKU

Jama’a suka ɗaga kai cikin mamaki.

Dukka yankunan sun taro an tabbatar da Prince Tarhim a matsayin sarautar sa

“Ban tursasa masa ba, ya aikata haka bisa adalci da tausayi kuma yanzu na yarda da zaɓinsa. Idan zuciyarsa ta karɓi Rahila, to hakan na nufin akwai wani ƙuduri na sama.”
Sanan Princeces Rahilat ta dawo daga muƙamin ta na asali yankunan mu na ƙarƙashin ta sarauta ɗaya ne kuma itace asalin jinin yankin Buga Afrika

Rahila ta ci gaba da zama ginshiƙi a masarauta, yayin da ake yawan kawo mata mata da yara don karɓar yaƙi  da shawara ta zama cikakkiyar Princess nata a inda ta rungume jarumin ta Tarhim domin a duniya idan akwai wanda take muradun to mijin ta ne shine asalin jarumin da take buƙatar kasance wa dashi tsawon rayuwar ta......

---
BACK TO STORY
BAYAN WATA

AJIYAR ZUCIYA

Ajiyar zuciya mai nauyi Ihsan ta sauke, yayin da ta buɗe idonta a hankali, idon ta kai ga duk sansanin da suka taru a kusa da wutar da suke zaune, idanun mutane sun cika da kewa, da kuma ƙaunar jin ci gaban labarin da ta kawo musu suna kallonta da nutsuwa, kamar sun manta da gajiyar hanya, yunwa da ɓacin rai tayi shiru na ɗan lokaci, sannan ta sake numfasa.

“Wannan shi ne labarin Princess Rahilat,” ta faɗa cikin natsuwa. “Ina fatan ya ɗan ɗauke muku

kewa a cikin wannan mawuyacin yanayi.”
duk suka jinjina kai sai Maryam ta ɗaga hannu cikin annashuwa.

“A gaskiya labarin ya kayatar, Ihsan. Amma ina da tambaya,” ta ce tana kallon ta kai tsaye. “Meyasa kike mana labari da Hausa da Turanci a haɗe?”

Ihsan ta murmusa, ta gyara zama kafin ta amsa.

“Hakika tambayar ki ta da muhimmanci Maryam domin shekaru fiye da dubu biyu da suka wuce, kafin turawa su shigo nahiyarmu, sukan ɗauki baƙaƙen fata tamkar bayi ne sun raina mu, sun mulke mu , amma akwai wani sarki mai suna Numan, wanda ya ƙwato yanki biyar daga hannun turawa, ya mayar da su 'yan ƙasa masu cikakken 'yanci.”

Ta dan yi shiru, tana kallon yadda idanu suka cika da sha'awa.

“Shi ya sa ya zama sarki na musamman a zamaninsa duk da kuwa mahaifin Rahilat azzalumi ne, amma saboda bajintarsa da yaki da turawa, aka ba diyarsa Rahilat sarauta – don ta ci gaba da kare mutuncin mutane kamar ku da ni. Wannan ne dalilin da ya sa nake haɗa Turanci da Hausa – domin har yanzu muna da ragowar tasirin turawan, amma da karatun irin wannan ne za mu dawo da mutuncinmu da fahimtar tarihinmu.”

Hannu suka sa, suka rungume ta duka daga gefe kuma Yazid ya ce da dariya:

“Wallahi, Ihsan, wannan tafiya tazo da darussa labarin Rahilat ya ɗaga min zuciya!”
John ya ɗora: “It’s like traveling into history and coming back with strength.”
Ado ya jinjina kai yana murmushi, “toh yanzu fa dai na tabbata, Ihsan ke ce jigo a cikin wannan tafiya, bari mu ci gaba da tafiya gobe, amma yau... yau dare ne na tunani.”

Suka kalli juna da murmushi, suka miƙe suna shirin kwana.

Daga can gefen zuciyar Ihsan, sai ta ɗan lumshe ido tana tunani:

"Bayan wata... akwai haske kuma wannan shi ne farkon komai."

continued by narnah ƙanwar soja ✍️✍️

https://chat.whatsapp.com/DoFR3n8lLtI1RB5Zd2z2IT

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON🌕

BY
NARNAH KANWAR SOJA
MARUBUCIYAR
MIJIN MAGE
FARASHIN SO
BIYAYYA GA UWA
DUHU CIKIN HASKE

RUHI BIYU
HANYAR RUWA
MAI CIKI CE
MADOBIN IDO
AHLIN LASHKAR
PRINCESSS RAHILAT
RAYUWAR UMMAH
BAYAN WATA

SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

Page 13/ 14
04 / 05 / 2025

بسم الله الرحمن الرحيم
اللهم صل على محمد وسلم

Maryam ta shafa gumi a goshinta, hannunta na rawa sai yanzu zafin jikin da ya ɗauke ta tun safe ya fara raguwa duk da haka, Idanunta sun ƙi buɗewa sosai, sai ihun zuciya da tafasar hawayen da take riƙe.

"Ihsan..." ta kira da rauni, "zan iya tafiya."

Ihsan ta rungume ta, hawaye na gangarowa daga idanunta. “kin ƙarfafa zuciyata fiye da yadda na zata,” ta ce cikin sanyi
Su Yazid, John da Ado sun zuba ido, zuciyoyinsu cike da yanke shawara basu da ƙarfi sosai,

amma lokaci yana guje musu.

“Yanzu ko ba yanzu ba ne idan  yanzu muka tsaya nan wata rana, za a cafke mu.” Yazid ya ce da ƙarfi, yana gyara jakar sa a bayansa.
sukai shiru  har sai da aka ji murya kamar ƙarar iska daga can nesa sai suka lumshe ido, suka lumshe zuciya.

Su biyar suka tattara kayan su da ƙarancin haske suka ratsa cikin duhu, gaban su cike da fargaba, amma babu wanda ya waigo baya,
Gabar boda na ƙasar Libiya ba kasafai ake iya shige ta da sauƙi ba. Rana ba ta faɗuwa sosai a hamada. Gashi da ke fesowa daga ƙasa kamar harshen wuta, yana fitar da zafi da ƙamshi irin na ƙasa mai mutuwa  babu bishiya, babu ruwa, sai yashi mai girma kamar kogon wuta.

Tsakanin dare da kwana biyu, sun ratsa titin ƙasa da ƙafa, su na bin jagorar wani tsoho wanda suka biya sauka-ka-tafi tsohon yana da hannu biyu kawai, amma gwaninta da sanin hanya sun fi soja da komfuta.

“Yanzu nan,” ya ce da ƙasƙantar murya yayin da suka isa ƙaramin rami da aka lulluɓe da dausayi. “Nan ne na ƙarshe kafin ku tsallaka Libiya. bayan nan, ba ruwa, babu tsaro kawai da zuciyar ku kuke tafiya.”
“Shikenan,” Yazid ya ce, yana gyara rigarsa. “za mu fuskanta.”

Maryam ta kama hannun Ihsan. “In muka tsallaka, to Allah ya bamu mafita.”
John ya lumshe ido. “I’ve never seen darkness this wide... but I feel hope.”
Suka shiga cikin hamadar da babu ƙyalli, suna tafiya suna shan iska mai zafi kamar wuta tana hura musu cikin hanci, cikin dare, rana tana walƙiya, ba saboda haske ba – sai saboda yashi yana motsi kamar ruwan teku.
Ado ya ce da jinjina kai, “wannan garin ba na mutane bane...”

“amma mu fa mutane ne da mafarki,” Ihsan ta ce, murya kamar zuma  “mu ma muna da hakkin tsira".
Zuwa wannan lokaci, tafiyarsu daga bodar Libiya ta ɗauki kwanaki, daga na farko zuwa na biyu, ƙarfinsu yana ragewa. Na uku sun fara kwana da cikinsu babu ruwa, babu abinci  rana ta huɗu, numfashinsu ya zama kamar na dabbobi, idanu sun ɗebe, fata ta bushe ta fara fashewa.

Hamadar Sahara ba fili bane na yashi kawai wani lokaci dutse ke cikinta, wani lokaci gami da

koguna da suka bushe shekaru da suka wuce amma duk inda suka kalli yanzu, sun haɗu da komai: rairayi masu santsi, ƙasa mai zafi, iska mai ƙarfi da tsintsiya da ke ɗagawa daga ƙasa har sama kamar baƙin hayaki.

Maryam ta fara jan ƙafarta a jikin yashi. takalminta ya dade da karyewa, yanzu ƙafarta bare – jajaye sun yi, cike da toka, ƙyalli daga rana. “Ihsan... ruwa... just one sip,” ta furta kamar mafarki.

Ihsan na bin ta da ido, kanta yana juyawa. Idanunta sun canza launi, sun zama kamar ƙwai, ba su da ƙyalli gashinta ya manne da gumi da ƙura, har ta daina jin sauyin iska. “Ba ruwa, ba komai amma ki tsaya Maryam... ki tsaya.”

Yazid yana gaba, yana rarrafe, yana fitar da numfashi kamar wanda aka sakar daga ƙarƙashin ruwa. John yana masa baya, amma yazo ƙasa. “I can’t feel my tongue...” ya ce da harshen da ya fara murɗewa.

Ado, wanda shi ke riƙe da jakar kowa, ya durƙusa. “I’m seeing mirages  I saw my mother – she was standing in water, calling me.”

Yashi ke rawa, rana ke ƙuna. Iska ta taso – iska mai nauyi, ƙamshi kamar zafi duka suka durƙusa, suka lulluɓe kansu da tsintsiya da kaya, amma iska ta kwashe su kamar hayakin gobara sun yi ta birgima kamar jakunkuna, har aka jefar da su zuwa wani ƙaramar rami – wani tsibiri a cikin sahara, tamkar tafkin dutse da ya bayyana daga ƙasa,  cikin haka suka faɗi su ka suma.

Wani lokaci daga baya...

Cikin ɓangararren inuwa da aka samu daga wata harsashen dutse, suka farka jikinsu a sanyi, amma cikin yashi babu ganye, babu ruwa, babu abinci. sai ga jikinsu ya fara nuna alamar rushewa – la'bbansu sun fashe, hancinsu ya bushe, idanunsu ba sa kallon juna, fatar hannu da ƙafa sun fara murɗewa, ta rikiɗe tamkar kaho

“Zan mutu,” John ya furta, yana kallon sama, “Ba ruwa  na sha fitsari na jiya ba zai isheni yau ba.”

Yazid ya kalli jikin sa, ya ji kamar naman jikinsa yana motsi. ya taɓa fatarsa – ta cire. “Wallahi mun gama.” ya fashe da kuka, amma ba kukan da kake ji  ba ƙara, sai hawaye masu zafi kamar gawayi.

Ihsan ta lumshe ido, ta kai bakinta ga wani ƙaho da ke ƙunshe da ragowar fitsari. ta sha kadan gaban Allah, ya fi komai wannan ba lokacin kunya bane, ko tsoron mutuwa. wannan yanayi ne da rayuwa take ƙi barin jikinsu , Maryam na jingine da dutse, tana kallon jikin ta kamar ba nata bane. “I’ve become sand,” ta ce. “Even my voice sounds like wind.”

Daga nesa...

Ado, wanda ya fi ƙarfinsu kaɗan saboda tsawon jikinsa da kwazon zuciyarsa, ya fara bin duwatsu da sandar da ya kakkarya bayan lokaci – sai ya hango wani abu wani rami mai zurfi da ke wani rami kamar tukunyar wuta. Yayi tsalle, ya kalla – ƙananan ragowar ruwa!
Yayi ihu kamar kura mai murna: “Ruwa! Wallahi, ruwa!” ya dawo da gudu yana faɗuwa, yana hura numfashi kamar za a sa wuta a jikinsa. “gashi chan ! gashi chan!”

Suna ta matsowa da karfin halin da ba su san inda ya fito ba. kowa da dabara, suka tsinke leda, suka tattara ƙwanƙwaso daga jikin su, suka kai bakin su... dan kadan, amma ceto. sannu a hankali zuciyarsu ta dawo  ba da kyau ba, amma da rayuwa suka kwanta, suka kalli sama, tsibirin da suke kai tsaye ne a tsakiyar Sahara, ba ruwa sosai, amma nan ne Allah ya basu mafaka.

Yazid ya ce da karamin dariya, “Idan muka tsira daga nan sai na ce duniya ba baƙi bane. duniya rana ce da yashi, amma ina da mafarki.”
Ihsan ta ce, “Na fi son mutuwa da mafarki  fiye da rayuwa babu buri.”
Maryam ta rufe idanunta " ya Allah mun gode maka da kyautar ruwa lallai ruwa zai rayu inda ba halitta amman mutum bazai rayu ba ruwa ba "..

Ruwan da suka tsinci ya zama tamkar aljanna. kowa ya samu ɗan kaɗan ya ji cikinsa ya huta. bayan kwanaki biyu a cikin wannan tsibirin – inda babu ciyawa, babu dabbobi, amma akwai inuwa da ƙaramin ramin ruwa – sai zuciyarsu ta ɗan dawo.

Ihsan ta janye rigarta mai sheƙi, ta taka da ƙafarta mai jini zuwa ga sauran su, ta ce cikin sanyin murya:
“Ku ji ni mana...”

“Mu ne matafiya,
Wanda ba su da gida,
amma zuciyarmu da rai,
suna cikin mafita...”
Maryam ta kama hannunta, suka fara juya da kasala, suna dariya da hawaye. Yazid da Ado suka buga ƙafa a yashi, John ya murɗa murya kamar yana wake, sai suka kama da karfi.

“Ruwan nan, ka ceci mu,
yashi da rana sun cinye mu,
amma muna raye,
muna tafe – cikin fata!”

Sai suka rungume juna – gaba ɗaya biyar – suna sharar hawaye, suna murza fatar jikinsu da suka rasa. Wannan rana ce da suka yi murmushi cikin azaba.

" Bayan wata akwai haske
Bayan wuya akwai daɗi "...

Bayan sati biyu a wannan wuri, ruwa ya kusa ƙarewa  sai suka yanke shawarar ci gaba da tafiya, domin sun san idan sun zauna za su mutu da yunwa da ƙishirwa. sun ɗaura jakarsu da fata, suka fito daga tsibirin suna zamewa a yashi.

Kwana biyu sun yi suna tafiya cikin rana da yamma. rana na dafa ƙafarsu, yashi na kai musu zafi daga ƙasa. idanuwansu sun fara ganin abu biyu, zuciyarsu ta fara shakku da juna. Maryam ta fara rikicewa, ta yi ihu tana zagin Yazid tana cewa:

“Ka ce zaka kawo mu Dubai! ka ce za mu ci kuɗi! Ashe ba haka bane?!”

John ya zube a ƙasa yana dariya da kukan hauka. “We’re already in Dubai – in hell's part!”
Ihsan da Ado suka kama su, suka kwantar da su kamar yara.

Bayan wata guda cikin tafiya da yunwa, sai suka hango wani gari daga nesa – amma ana shigarsu kusa da shi sai suka ji hayaniya. mutane masu bindiga da dabbobi ke yawo a kusa – mafarauta ne amma ba na noma ba – ‘yan fasa-ƙwauri ne da ke farautar masu tsallaka haddi don su sayar da su ga masu aikatau ko masu fatauci.

Sun kamasu a dare sun ɗaure su da igiya, suka ajiye su a cikin wani daki tamkar kurkuku da yashi a ƙasa. Maryam ta fara kuka, John ya yi shiru yana kallon su kamar wanda ya hakura da rayuwa. Yazid ya yi ƙoƙarin fita, aka yi masa dukan tsiya, aka zubar da jininsa.

Ihsan da Ado sun tsaya suna kallon juna da hawaye. Ado ya ce:
“Na rantse, idan muka tsira daga nan, ko ruwa ne, ko wuta, zan kawo ki gida da hannuna.”
Ihsan ta runtse ido. “Zan riƙe ka da zuciya har ƙarshe.”

Continued .............
by narnah ƙanwar soja ✍️✍️

https://chat.whatsapp.com/BsQ0CkOCA83FgwnQ177z9y

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON🌕

BY
NARNAH KANWAR SOJA
MARUBUCIYAR
MIJIN MAGE
FARASHIN SO
BIYAYYA GA UWA
DUHU CIKIN HASKE
RUHI BIYU
HANYAR RUWA
MAI CIKI CE
MADOBIN IDO
AHLIN LASHKAR
PRINCESSS RAHILAT
RAYUWAR UMMAH
BAYAN WATA

SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

15 / 16
08 / 5/ 2025

Kamar yadda aka saba duk shekara, Alhaji Saminu bai taɓa yin ƙasa a guiwa ba wajen nuna ɗimbin darajarsa a idon mutanen ƙauyen Gembò amma wannan karon daban ne. wannan karon ba kawai don shanaye ya zo ba ya zo ɗaukar amana.

A gaban Moddibbo da wasu dattawan gari guda biyu, Alhaji Saminu ya fito da sadakin Halima. kudi ne masu yawan da fulani ba su fiye gani ba a lokaci guda baya ga hakan, ya kawo 'yan dabbobi da kayan gyaran amarya, tare da alkawarin dawowa bayan Sallah da sati biyu—kai tsaye daga birnin Tarayya Abuja inda matarsa ke zaune.

Moddibbo ya karɓi sadakin cikin nutsuwa da girma ya san me hakan ke nufi: yanzu Halima zata koma karkashin Alhaji Saminu amma ko da yake zuciyarsa na cike da nauyin amana, bai nuna ba, saboda a rayuwa irin tasu, alƙawari tamkar doka ne da ba za a karya ba.

Halima kuwa... ta zauna a gefen mahaifinta da cike da kunya, fuska a kasa kamar yadda aka koya mata, duk da cewa an ba ta labarin cewa rayuwar birni ce zata zame mata gaba, kuma Alhaji Saminu mutum ne mai arziki da daraja—amma a zuciyarta babu motsin soyayya ko ɗokin aure.

Zuciyarta tamkar fili ne, babu shuka, babu furanni kawai akwai wata siririyar lafazi da take maimaitawa a ranta:

"Na yarda da mahaifina na amince da kaddara. kuma zan bi Alhaji Saminu, ko da zuciyata ba ta motsa ba."

Irin wannan biyayya ce da ta sa ta karɓi sadakin da lafazi guda biyu:
“Na yarda.”

Moddibbo kuwa kamar kowa yana ganin yana murna amma shi da zuciyarsa sun san gaskiya , ya  san Halima ba ta kai matsayin aure ba tukuna ta girma da sauri, amma zuciyarta har yanzu karama ce, tamkar macen da bata fara sanin al'amuran soyayya ba.

Sai dai kuma, Moddibbo mutum ne mai daraja da mutunci ya rike amanar Alhaji Saminu fiye da yadda wasu ke rike 'ya'yansu. Yana fatan Alhaji Saminu zai kare martaba da tsaron Halima kamar yadda ya rike alkawari na shekaru goma sha biyar.

Wani iska ya buso daga arewa, ya kada ganyen kuka da ke bakin ruga Halima ta lumshe ido, tana jin iskar kamar wata alama ce daga sama ko soyayya zata zo daga baya? ko kuwa hakan nan ne rayuwa ta rubuce mata?

Bayan sati biyu da cikar alkawari, ƙauyen Gembò ya sake fuskantar wata rana da ba za a taɓa mantawa da ita ba rana ce da komai ya sauya—rana da tarihi ya ƙara rubutun zinariya cikin ƙwarya mai ƙyalli.

A safiyar ranar asabar, tun ƙarfe tara da mintuna goma, sai ga jere-jeren motoci guda shida masu sheƙi da ƙyalli irin wanda bai saba zuwa ƙauyen ba, motoci ne kirar Lexus LX 570 guda biyu, guda bakar fata, guda kuma fari ɗan haske mai cike da adon zinariya. Sauran kuwa motoci ne kirar Hilux da Toyota Highlander, dukkansu cike da kaya, kujerun zamani, manyan jakunkuna da akwatuna masu lulluɓe da furen ado da yajin rawaya.

A wata ƙaramar Prado, wanda aka ɗora babban laifan jajjayen furanni da tutar Kaunar aure, Alhaji Saminu ne ya fito sanye da babban ɗan-baban Shadda mai launin zinariya da ruwan hoda , babbar hula ce ta fulani bisa kansa, mai ɗinki na musamman da adon sarka fitarsa daga mota ta sa yara suka yi tsalle, mata suka fara cewa:

“Ga angonmu ya iso! Allah ya sa a dace!”

Shi kuwa, yana da murmushin da ba'a san a zuciya akwai tsoro da jin nauyin amanar da ya ɗauka ba bayansa, abokansa biyu da shaidu—Alhaji Babangida da Alhaji Laushi—duk sun fito cikin kayan zamani ƙauyen ya sha ado kamar an shirya masa sallah  gari ya ɗau shela da kade-kade na kalangu da waka:

“Alhaji Saminu yazo!
angon Halima yazo!”

Tun daga makon da ya wuce, iyayen Halima sun ɗora shagalin al'ada, mata na unguwa sun taru kullum ana sallake, ana gasa binkami, koskoso, da kilishi. Halima tana zaune cikin ɗakin mahaifiyarta marigayiya, cikin duhun tunani da zumudin rayuwar da ba ta san me take cike da ita ba ,aka yi mata lalle, aka sa mata ƙwarya ta ruwan turaren wuta a gefenta, aka shafa mata manshanu a fata, aka ɗinke mata zani da riga mai alamar Fulani na gargajiya—jar zani mai adon ratsi da santali na tsaf.

An saka ta cikin wani ɗaki mai ƙyalli da kilishi, ana yayyafa mata ƙamshi da bakhour, ana duba fatarta da gashinta, yarinyar ce kyakkyawa da kyau na halitta, ba ado ke ƙawata ta ba—rashin yawan maganganu da nutsuwar ta ce abin kallo.

A gaban limamin ƙauye da shaidu, aka daura auren Halima da Alhaji Saminu da sadaki naira dubu ɗari biyar, da sarkar zinari da kayan gida., adaidai lokacin da aka furta "na ɗaura", Halima ta fashe da kuka mai ƙarfi. Sai dai ba kuka na soyayya ko jin daɗin aure ba ne—kuka ne na rabuwa da matar mahaifinta, wacce ta raineta tun rasuwar mahaifiyarta, wani kuzarin tunani ya cika ta, kamar tana jin kamar yanzu rayuwarta ta sauya daga yarinya zuwa amarya, daga ƙauye zuwa birni.

Moddibbo ya share hawayen sa da alwala, yana murmushi mai cike da damuwa, yana fatan Halima zata dace da sabon rayuwar da zata tafi ciki, a zuciyarsa yana fatan Alhaji Saminu zai rike ta fiye da yadda aka rike ’yar sarki.

Alhaji Saminu ya bar ƙauyen ba da hannu ba. Ya bar da ɗimbin kyaututtuka: kudi ga matan unguwa, jakunkunan shinkafa, kayan abinci, sabbin riguna da ɗinkin zamani ga matasa, har da jakunkuna ga yara da aka ce "na makaranta".

Wajen fitarsu, aka shigo da sabuwar amarya cikin sabuwar rigar aso-ebi da kwalliyar santali,

aka ɗaura mata gyale mai nauyin zinariya, aka raka ta da kalangu da wake-wake, aka saka ta cikin motar farin Lexus, sai ga kafila ta nufi birnin Abuja.

Amarya ta fito daga ƙauye—amma fuskarta na cike da tambayoyi. Shin me birnin ke ɓoye mata? Me Alhaji Saminu zai kasance gareta? shin wannan aure zai fassara soyayya ne, ko wata kyauta ta biyayya ce da ba zata taɓa jin daɗin ta ba?

*********************************

Juyawa tayi da ƙarfi kamar wadda aka hangi zuciyarta ta nitse cikin ruwan kogin ɓacin rai. tana mai huci da numfashi mai nauyi, ta faɗa jikin Moddibbo kamar jaririya, ta rungume shi da ƙarfi, tana kuka mai girgiza zuciya dukkan gangar jikinta na rawar jiki, murya na rawa kamar ana buɗe gidan hawaye a zuciya.

Moddibbo ya kama kanta yana bubbuga bayanta da hannunsa mai sanyi da tausayawa. "Allah ya sa ki dace Halimatu," ya faɗa da wani murya da yafi shiru nauyi. "ki rike mutunci, ki tsaya da imani kiye koyar da mahaifiyar ke a fagen haƙuri zaki ci ribar zaman duniya ... rayuwa ce bata da tabbas."

Shi kansa idonsa cike da ruwa, kodayake zuciyarsa ta taɓu sosai—ya jima yana kallon Halima tamkar zinariyar sa wanda yanzu ya mika hannunsa ya mika ta ga duniya. ya mika al'amuranta ga wani mutum da ya fi shi daraja da kima, amma ba shi da tabbacin soyayya.

Bayan kuka da ban kwana mai cin rai, sai Halima ta shige cikin motar Alhaji Saminu da zuciyar da ba a iya fassara. Alhaji yana ƙoƙarin rarrashi da annuri, yana ƙyalƙyala dariya mai taushi yana faɗin:

"Amaryata kada ki damu, Abuja ba abin tsoro ba ne ke zauna lafiya, za ki ga alheri."

Halima bata ce komai ba ta  fuskanci gilashin motar tana kallon ƙauyen su da ke raguwa a bayanta kamar mafarkin da ya ɓace. hannunta na cikin haɗaɗɗiyar rigarta, amma zuciyarta na cikin tsohon zanin ƙauyenta.

Motoci suka fice daga Gembò, suka fasa hanyoyi masu kura, suka dosa garin Yola inda jirgi zai tashi zuwa Abuja. Halima na zaune cikin mota, amma kamar a mafarki ta kasa kallon sabbin gine-gine da suka wuce su, kamar ba su da ma'ana gareta.

A lokacin da suka isa filin jirgi, an ce mata  "Halimatu! Ki sauka ",ta  sauka cikin rigima, tana kallon ƙasa kamar tana tsoron ƙasa ce zata buɗe ta haɗiye ta ba ta san me ake nufi da "ticket" ba ba ta san yadda ake biya ba yanzu ne Halima ke fara jin bambancin rayuwa, ta kasa cire takalmanta a wajen sakan na'ura, sai da ma'aikaciyar ta fara dariya ta ce:
"Yarinya! ba salla za ki ba  wannan tsafta ne da dokar jirgi."
taji kunyarta sosai  ldonta ya cika da ƙyama da tozarta a zuciyarta:
"kai! ashe akwai duniya kamar haka?"

Bayan an kaita cikin jirgin, aka ɗaure mata seat belt, ta riƙe kujerar kamar wacce ke cikin ruwa mai zurfi. Da jirgi ya tashi, ta saki ƙara mai firgitarwa:
"Innalillahi wa inna ilaihi raji'un! Wayyo Moddibbo…! na mutu!"
Alhaji Saminu ya riƙe hannunta da dariya "babu komai Halimatu, jirgi ne ke tashi kawai."

Kamar sabuwar tsuntsuwa aka ɗauke daga ciyawa, aka ajiye cikin gini mai fanfo. As zuciyarta, birni kamar wata. Amma tambaya ɗaya ke ci mata rai: Shin wannan sabon garin da take ciki zai taimake ta ta samu sabuwar rayuwa, ko zai ɓata mata tunanin da take tsaye da shi tun ƙuruciya?

Tunda suka hau cikin jirgin sama, Halima ta kasa zaman lafiya idanunta na zagaye cikin hadadden komai wanda ba ta taɓa mafarkin wanzuwarsa ba , tana kallon tagar gefe, tana ganin sararin samaniya da ƙasa na raguwa kamar yadda aka rage wa tunaninta hankali. amma wani abu ya sake ɗaukar mata hankali...

A kujerar bayan nata, wani saurayi ne zaune, ya murtuƙe fuska, idonsa kamar na damisa mai zurfin tunani , fuskar sa doguwa ce, fara tas kamar bulo, ƙuncinsa yana da ɗan launin ja, bakinsa siriri ne amma mai ɗan ƙasaita  gashin kansa an rage shi tsaf yana sheƙi, sai karan agogon zinare a hannunsa na hagu ya ƙara ɗaukar hankali.

Shima yana kallon Halima, ba da sha'awa ba, amma da mamaki da tausayi kadan kamar yana cewa da kansa, "Ina aka samo irin wannan 'yar ƙauye mai tarin kamala?"
suna cikin tashi ne Halima ta saki ihun da ya gigita kowa
"Wayyo Allah naaa! waye ya ce jirgi zai ɗaga?! Innalillahi wa inna ilaihi raji'un!"

Mutane sun juya suna kallonta, mata suka dinga dariya a nutse, wasu kuma suka tausaya amma shi saurayin da ke baya—ya kalli fuskarta da jajayen idanu, yana juyar da kansa a hankali cikin murmushin gefen baki, kamar wanda ya saba da irin haka a rayuwar zuciyarsa , sun sauka a filin jirgin Abuja, wanda ya bude musu sabon shafi a rayuwa.

Alhaji Saminu ya nufi Maitama da su, inda katafaren gidansa ke cike da girma da kima. gidan na da kofa babba mai lanƙwasa kamar ƙofar masallaci a Makka. farfajiya ce a waje, da lambu mai yalwa, sai tsuntsaye ke ta raira waka kamar sun san sabon baƙuwa ta iso.

Yayin da Halima ta kalli ƙofar katafaren gidan, zuciyarta na wani irin doki da tsoro da fargaba, wani sashe na ruhinta na faɗin "kin fito daga ƙauye, amma an jefa ki cikin birnin masu hannu da shuni..." da zuciya ɗaya ta shiga, sanye da kayan aure na gargajiya: mayafin fulawa, zobba a yatsu, da dankwali mai yatsin zinariya.

A cikin gida, motoci sun sha jerin gado, masu gadin gidan biyu a ƙofar shigowa suna miƙa gaisuwa da ban girma. Gidan kuwa – katafaren alfarma ne wanda ba a taɓa mafarkin Halima zata taka kafarta ciki ba. Babban falon yana da manyan tagogi masu labulen fata na turkiyya, cike da fitilu na chandelier masu hasken zinariya, cikin falon ne Hajiyah Nafisa ta karɓe ta da murya mai cike da mamaki:

Matar Alhaji Saminu, Hajiyah Nafisa, ta fito sanye da kayan alfarma gashinta a jikin mayafi yana sheƙi kamar rigar sarauta ta kalli Halima da murmushi na ɗan lokacin, amma idanunta na cike da alamun tambaya:
"Itace wannan yarinyar?"
Halima ta kasa magana ganin palon gida kadai ya isheta tiles ne na zinariya da hoda mai sheƙi, fanfo a bango da tebur na gilashi. tana takawa kamar ana binsa da ƙasa. Zuciyarta na cewa:
"To wallahi... haka birni yake ko dai na mutu ne an kawo ne gidan aljanna ?" kwalliyar da aka yi mata da kayan Fulani na auren ƙauye—maye da zobe da mayafi na fulawa—ya sa ta ƙara haske , amma a fuska akwai shakku, akwai salo na "ba sani ba sabo." sai dai akwai mutunci a tafiyarta, wanda ba'a koya shi a birni.
"Nafisa itta ce amaryata na biya sadakinta tun can ƙauye kamar yadda na gaya miki. Allah yasa alkhairi."
Hajiyah Nafisa ta tabe baki cikin murmushi mai nauyin fahimta daga kallon ta ɗaya ka gane ko da tana ƙoƙarin karɓarta, zuciyarta ba ta cikin hakan gaba ɗaya.

Sai da aka kai ta ɗakinta da aka tanadar mata cikin gida ɗaki mai faɗi sosai, bangon sa mai launin cream da zinariya an shimfiɗa masa carpet mai laushi, akwai gado babba da labule mai juyawa kamar na sarauta taga biyu na dakin suna kallon lambun cikin gida, inda tsuntsaye ke ta shawagi, cike da kyan gani. dakin na da fanka da AC, amma Halima bata san amfani da komai ba. Sai kallon su take kamar kayan sihiri.

Ta zauna a gefen gado daidai lokacin wata mai aiki – Hasiya – ta shigo da murmushi a fuskarta. Hasiya daga Sokoto ce, mai ƙanƙantar jiki da zubin kawaici atake suka fara haɗuwa Hasiya ta ce da ita:
"Wallahi Aunty Halima kin yi kyau, da gaske ne ke daga ƙauye?"

“Eh... daga Gembo,” ta ce da dariya mai daɗin ji. “kin taɓa jin sunan kauyen?”
“A'a, amma yanzu na ji ki. sai dai ki gyara nan Abuja fa ne Idan baki yi wayo ba, sai a cuce ki.”

Nan suka fara zama ƙawayen gaske. Halima ta fara ɗan sabawa cikin gidan, musamman da yaran Alhaji Saminu goma da ke gidan. akwai Muneerah da Ruqayyah – ‘yan mata manya masu haɗe da kwalliya da rashin kunya, masu jin turanci da yi wa Halima kallon kamar uwar kauye suna kiran ta “that girl from bush” a bayan ta.

Sannan akwai Aminu Junior da Zaid, samari matasa da suka fi ɗaukar lokaci a wajen gidan basu damu da sabuwar mace, sun fi shagaltuwa da motocinsu da rayuwar club da Instagram.

Yara uku ƙanana—Sulaiman, Abbas, da Fadilasun fi sabawa da Halima suna zuwa ɗakinta suna wasa da ita ta dinga yi musu wasan shanu da dabbobi da kida da rawa irin na ƙauye, suna dariya kamar an saka musu annashuwa a zuciya tana ɓoye wannan zumunci da su domin kada uwayensu su ji.

Matar biyu kuwa, Hajiyah Mariyah da Hajiyah Sabeerah, su ne abokan huldar Nafisa amma Hajiyah Mariyah ce shaidaniya, mai haƙurin fitina da halin mugunta tana kallon Halima da kyankyami, tana cewa:
“Wato wannan ƙaramar ‘yar Fulani ce ta zo mana da daddare? Allah ya sa ba za ta ja mana Alhaji ba.”

Tun daga rana ta fara tsara yadda zata nunawa Halima cewa gidan ba da sauki ba ne. tana tura mata ayyuka kamar ba matar aure ba: “ki share wancan, ki gyara kicin, ki tafi can ki goge banɗaki.”

Halima kuwa, da jin kunyar Fulani da biyayya, sai ta dinga yi tana mika hannu da zuciya, ba tare

da kuka ko korafi ba inda Hasiya ta fi shiga tsakiya, tana mata nasiha da rarrashi:
“Ki yi haƙuri Halima, nan ne birni idan kika nuna rashin juriya, sai su hana ki kwanciyar hankali amma Allah yana tare da mai gaskiya.”

A haka Hajiyah Nafisa ta dinga kallon yadda Halima ke yi wa yara wasa, tana girki da kyau, tana wanke-wanke da murmushi da farko tana kyamar ta, amma wata rana ta shigo dakin Halima sai ta ganta tana dinki wa Fadila riga da hannu wani abu ya motsa a zuciyarta. Ta ce da kanta:
“Wannan yarinyar... ba ta da mugunta kuma girmanta yana shigowa hankali.”

Halima kuwa har yanzu bata san haka ba. zuciyarta na yawo ne da tambayoyi: “shin wannan rayuwar ita ce rabona? ina mahaifina da mahaifiyata? W
wannan Alhaji Saminu fa, me yasa yake sona?
wani dalili ne yasa ya kawo ne gidan sa ya ajiye tsawon lokaci bai dawo garine ba?

Ohhhhhhhh ga Halima ga Abuja
a sannu a hankali zamu shiga labarin Halima

continued ƙanwar soja in Sha Allah

✍️

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON🌕

BY
NARNAH KANWAR SOJA
MARUBUCIYAR
MIJIN MAGE
FARASHIN SO
BIYAYYA GA UWA
DUHU CIKIN HASKE
RUHI BIYU
HANYAR RUWA
MAI CIKI CE
MADOBIN IDO
AHLIN LASHKAR
PRINCESSS RAHILAT
RAYUWAR UMMAH
BAYAN WATA

SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

15 / 16
07/ 5/ 2025

Iskar hamada ta na kada yashi cikin karfi, tana fasa fuskokin su da ƙaƙƙarfar zafi gaban su babu

komai sai fure-furen duhu da tsayayyun ciyayi waɗanda rana ta ƙone su har sun bushe. kusan ko motsi ba ya sake yi sai idan iskar ta kaɗa su kamar wasu fatalwun da ke kaɗa hannunsu don ƙiran mutuwa.

Jiki duk jini, ruwan jiki ya bushe. Fuskarsa ta kumbura, leɓɓansa sun fashe saboda ƙishi da rana dukansu suna daure cikin zafi da juna,  Yazid ya ɗaga kai da wahala, yana wani tunani kamar wani ɗan ruhi mai kaifin fahimta, ya fara rerawa da wata murya mai kauri wadda ke ɗauke da ƙyamar wahala:

"Bayan wata...
bayan wata akwai haske
Bayan dare akwai rana
a duhun daji babu alheri,
a zuciya babu tsira..."

Waƙar ta ja kunnensu gaba ɗaya. Ihsan ta ɗan kai hannu ta shafi kafadarsa, Maryam ta rungume ƙirjinta, tana kokarin hana kuka.
"ku shirya..."  Maryam tace a hankali, murya kamar tana fitowa daga wani daki mai ƙyama. "Zan baku labarin soyayya  "
suka gyara zama, sun sha wahala, "  amma labari na da ƙarfi fiye da na ihsan domin wanan labarin soyayya  da  butulci  cin amana da nishadi yana da matukar muhimmanci a yanayin da muka  tsinci kanmu "

Maryam ta sauke ajiyar zuciya mai nauyi, tana kallon abubuwan da suka gabata a cikin zuciyarta a  yau, ta yanke shawarar cewa lokaci ya yi da za ta bayar da labarin  soyayya. Labari wanda ba kawai soyayya ba ne, har ma yana da cike da butulci,  tausayi da ƙalubale, wannan labarin yana da ban sha'awa, cike da nishadi, kuma yana dauke da darussa masu nauyi ga wanda zai saurara “amma soyayya ba ta tsaya a nan ba,” Maryam ta ce, tana dariya. “duk da haka, akwai abubuwan nishadi, da tausayi.

( Lokaci yayi da zamu shiga labari cikin labari Maryam zata bamu labari a cikin tafiyar su na Bayan wata a inda aka mafarauta suka kama su ,suna tafiya dasu cikin wahala da zafin rana da yunwa )..

RUGAR FULANI

Rugar tana cikin zurfin dajin Arewa maso gabas, cike da ciyayi kore-kore da ke motsawa cikin sanyi na safe gidajen su cike da tsari na gargajiya, daga bukkoki masu rufi da itatuwa da kwari na fulawoyi masu ƙanshi. a gefe akwai madugu mai fitowa daga tsauni, yana gangarowa zuwa tabkin da shanun su ke zuwa kowane safe a cikin rugan ana jin karajin shanu, da waƙar kiwo da yara ke rerawa, kowane gida na da kangon dabbobi, da inda matan gida ke nono da jujjuya fura.

Sunanta Halima, kyakkyawa ce tamkar wata a tsakiyar dare idanunta farare ne masu zurfi, suna ɗaukar hankali da kyalli mai launin kwayar gwal fuskarta farin fata ce kamar nonon shanu, tana da dogon hanci da siraran leɓɓa  gashinta baƙi ne da sheƙi, an nade shi cikin ɗamara ta Fulani mai launin ja da zinariya tana sanye da zanne mai ɗinki na gargajiya, da ƙyarar kunne na azurfa, da zobba masu sarkar ƙaho tana da shekaru goma sha biyar, amma hankalinta da nutsuwarta sun fi na shekaru.

Halima tana da ƙwarewa wajen kiwon shanu, ta san kowanne suna, kuma tana iya busa algaita

da wake-waken daji da suka gada. Tana da natsuwa da ladabi, amma cikin zuciyarta akwai mafarkin soyayya da birni, duk da tana jin kunyar faɗa ,a  kullum tana kallo daga gefen ruga tana mafarkin rayuwa mai zurfi, tana ɗora fatarta kan murya da waƙar wani saurayi da ya taɓa tsayawa bakin tabki yana kallo duk da cewa bataye ilimin zamani ba amman tabass tana da ilimin addini da ilimin sanin halayyar ɗan Adam

Kamar yadda kowacce shekara take kasancewa, haka wannan shekara ma ta zo da nata alkawura ,daga nesa, ƙura ta fara tashi. Yara suka fara ƙwala ihu suna fadin:
"ga motar Alhaji! ga motar Alhaji!!"

Motoci biyu Honda guda fari da ɗaya baki  suka bayyana cikin natsuwa, suna karasowa cikin ƙauyen Gembo Saƙa-saƙan ƙura ke biye da su, kamar girgijen albarka. dun tsaya kai tsaye a gaban bukkar Moddibbo, wanda shi ne babba kuma mai daraja a wannan yanki wata irin lumana da nutsuwa ke lullube daƙalin gidan nasa, kamar yana jiran zuwan ɗan sarki.

Alhaji Saminu ya fito daga motar fari cikin dogon riga shadda mai launin zinariya, da rawanin da ke sa hasken rana ya bayyana a goshinsa. Murmushin sa na cike da annuri, yana ɗaukar zuciyar kowa da kallo kallonsa kaɗai na saka mutum jin kwanciyar hankali.

Moddibbo kuwa, ya fito da kansa daga cikin ɗakinsa, cikin natsuwa irin ta dattijo mai hangen nesa. Suka runguma kamar ’yan

Moddibbo kuwa, ya fito da kansa daga cikin ɗakinsa, cikin natsuwa irin ta dattijo mai hangen nesa. Suka runguma kamar ’yan uwa da suka jima ba su hadu ba. baiwa da mutunci sun kasance tsakanin su tun shekaru goma da suka wuce — alaƙar da ba kuɗi ko matsayi ba ne ya ɗaure, illa kirki, imani da gaskiya.

“Barka da zuwa, Alhaji,” Moddibbo ya furta cikin murya mai nauyin daraja.
“Lafiya lau, Moddibbo. Allah ya tabbatar da alheri kamar kullum,” Alhaji Saminu ya amsa da

ladabi.

Maza da yara sun fara taruwa a kofar gida, ana kallon motoci da murmushi, yayin da matasa ke harhada shannaye daga gindin kuka da ke kusa da gona, domin Alhaji ya saba fita da kansa yana zaɓar dabbobin da zai yanka domin hidimar Sallah ga iyalansa da maƙwabta.

Bayan doguwar gaisuwa ta mutunci da girmamawa tsakanin dattijan biyu, sai ga Halima yarinya mai kyaun da ke bayyana a hankali kamar safiya mai sanyi ta fito da kwanon madara a hannunta, fuskarta daɗaɗɗiya, idonta mai cike da nutsuwa, ta isa gaban baƙi cikin kamewa da girmamawa.

"Assalamu alaikum," ta faɗa da siririyar murya

"Wa alaikumus salam," Alhaji Saminu da Moddibbo suka amsa a tare, suna kallonta.

Alhaji Saminu ya karɓi madarar hannunta, yana dubanta cikin ido da murmushi da ke ɓoye wani sirri mai zurfi. Halima ta sunkuyar da kanta, tana juyawa cikin girmamawa kamar yadda aka koya mata.

Bayan ta shige ciki, Alhaji Saminu ya ɗan juyar da kallonsa zuwa ga abokin zamansa. "Moddibbo... shekarun Halima sun cika goma sha biyar yanzu, ko ba haka ba?"

Moddibbo ya gyara zamansa, ya ɗan sosa gemunsa yana murmushi mara kyar.

"Eh, haka ne. shekaru goma sha biyar rabon da ka min wannan alkawarin."

Alhaji ya lumshe ido. "Na tuna sosai ka ce Halima zata zamo matata, kuma kai da kanka zaka miƙa min ita ranar da ta kai munzalin aure."

Moddibbo ya ɗan sauke ajiyar zuciya, yana kallon ƙasa.

"Ka sani Alhaji... ban taɓa mantawa da alkawarin nan ba. kuma na tsaya akan shi har yau saboda girmanka da darajarka a idona. Amma fa mutane sun fara tambaya, sun fara zargi... wasu na cewa wai ni na hana Halima aure saboda son zuciya wasu ma na ganin kamar ina fuskantar matsin lamba daga wani ɓangare."

Alhaji Saminu ya ɗan sunkuyar da kai, muryarsa na nuna laushi da tausayawa.

"Moddibbo... ka sani Halima tana da muhimmanci a gareni fiye da yadda za a iya fassarawa da baki amma idan hakan zai cutar da mutuncinka ko na yarinyar... sai mu sake duba hanyar da za a bi cikin adalci da amana."

Moddibbo ya ɗan kalli tsohon abokinsa, yana girgiza kai da murmushi mai ɗan nauyi.

"Alhaji, ni dai ba zan karya alkawari ba kuma Halima ma ta san da cewa tana da wani babban makoma da muke jiran lokaci ina so a kyautata komai cikin tsari da girmamawa... da zarar ka ce lokaci yayi—ni a shirye nake."

Alhaji Saminu ya ɗaga kai, idonsa na ɗauke da abu fiye da kalmomi.
"To lokaci yayi, Moddibbo kuma Halima zata dawo gareni—amma ba kawai a matsayin amarya ba, a matsayin amanar da zan ci gaba da kulawa da ita kamar zinariya mai tsarki."

Get ready fans ga Halima ga Alhaji Saminu menene abinda wannan gajeren labarin Maryam ya ƙunsa , let's go..........

https://chat.whatsapp.com/BsQ0CkOCA83FgwnQ177z9y

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON🌕

BY
NARNAH KANWAR SOJA
MARUBUCIYAR
MIJIN MAGE
FARASHIN SO
BIYAYYA GA UWA
DUHU CIKIN HASKE
RUHI BIYU
HANYAR RUWA
MAI CIKI CE
MADOBIN IDO
AHLIN LASHKAR
PRINCESSS RAHILAT
RAYUWAR UMMAH
BAYAN WATA

SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

15 / 16
08 / 5/ 2025

Kamar yadda aka saba duk shekara, Alhaji Saminu bai taɓa yin ƙasa a guiwa ba wajen nuna ɗimbin darajarsa a idon mutanen ƙauyen Gembò amma wannan karon daban ne. wannan karon ba kawai don shanaye ya zo ba ya zo ɗaukar amana.

A gaban Moddibbo da wasu dattawan gari guda biyu, Alhaji Saminu ya fito da sadakin Halima. kudi ne masu yawan da fulani ba su fiye gani ba a lokaci guda baya ga hakan, ya kawo 'yan dabbobi da kayan gyaran amarya, tare da alkawarin dawowa bayan Sallah da sati biyu—kai tsaye daga birnin Tarayya Abuja inda matarsa ke zaune.

Moddibbo ya karɓi sadakin cikin nutsuwa da girma ya san me hakan ke nufi: yanzu Halima zata koma karkashin Alhaji Saminu amma ko da yake zuciyarsa na cike da nauyin amana, bai nuna ba, saboda a rayuwa irin tasu, alƙawari tamkar doka ne da ba za a karya ba.

Halima kuwa... ta zauna a gefen mahaifinta da cike da kunya, fuska a kasa kamar yadda aka koya mata, duk da cewa an ba ta labarin cewa rayuwar birni ce zata zame mata gaba, kuma Alhaji Saminu mutum ne mai arziki da daraja—amma a zuciyarta babu motsin soyayya ko ɗokin aure.

Zuciyarta tamkar fili ne, babu shuka, babu furanni kawai akwai wata siririyar lafazi da take

maimaitawa a ranta:

"Na yarda da mahaifina na amince da kaddara. kuma zan bi Alhaji Saminu, ko da zuciyata ba ta motsa ba."

Irin wannan biyayya ce da ta sa ta karɓi sadakin da lafazi guda biyu:
“Na yarda.”

Moddibbo kuwa kamar kowa yana ganin yana murna amma shi da zuciyarsa sun san gaskiya , ya san Halima ba ta kai matsayin aure ba tukuna ta girma da sauri, amma zuciyarta har yanzu karama ce, tamkar macen da bata fara sanin al'amuran soyayya ba.

Sai dai kuma, Moddibbo mutum ne mai daraja da mutunci ya rike amanar Alhaji Saminu fiye da yadda wasu ke rike 'ya'yansu. Yana fatan Alhaji Saminu zai kare martaba da tsaron Halima kamar yadda ya rike alkawari na shekaru goma sha biyar.

Wani iska ya buso daga arewa, ya kada ganyen kuka da ke bakin ruga Halima ta lumshe ido, tana jin iskar kamar wata alama ce daga sama ko soyayya zata zo daga baya? ko kuwa hakan nan ne rayuwa ta rubuce mata?

Bayan sati biyu da cikar alkawari, ƙauyen Gembò ya sake fuskantar wata rana da ba za a taɓa mantawa da ita ba rana ce da komai ya sauya—rana da tarihi ya ƙara rubutun zinariya cikin ƙwarya mai ƙyalli.

A safiyar ranar asabar, tun ƙarfe tara da mintuna goma, sai ga jere-jeren motoci guda shida masu sheƙi da ƙyalli irin wanda bai saba zuwa ƙauyen ba, motoci ne kirar Lexus LX 570 guda biyu, guda bakar fata, guda kuma fari ɗan haske mai cike da adon zinariya. Sauran kuwa motoci ne kirar Hilux da Toyota Highlander, dukkansu cike da kaya, kujerun zamani, manyan jakunkuna da akwatuna masu lulluɓe da furen ado da yajin rawaya.

A wata ƙaramar Prado, wanda aka ɗora babban laifan jajjayen furanni da tutar Kaunar aure, Alhaji Saminu ne ya fito sanye da babban ɗan-baban Shadda mai launin zinariya da ruwan hoda , babbar hula ce ta fulani bisa kansa, mai ɗinki na musamman da adon sarka fitarsa daga

mota ta sa yara suka yi tsalle, mata suka fara cewa:

“Ga angonmu ya iso! Allah ya sa a dace!”

Shi kuwa, yana da murmushin da ba'a san a zuciya akwai tsoro da jin nauyin amanar da ya ɗauka ba bayansa, abokansa biyu da shaidu—Alhaji Babangida da Alhaji Laushi—duk sun fito cikin kayan zamani ƙauyen ya sha ado kamar an shirya masa sallah  gari ya ɗau shela da kade-kade na kalangu da waka:

“Alhaji Saminu yazo!
angon Halima yazo!”

Tun daga makon da ya wuce, iyayen Halima sun ɗora shagalin al'ada, mata na unguwa sun taru kullum ana sallake, ana gasa binkami, koskoso, da kilishi. Halima tana zaune cikin ɗakin mahaifiyarta marigayiya, cikin duhun tunani da zumudin rayuwar da ba ta san me take cike da ita ba ,aka yi mata lalle, aka sa mata ƙwarya ta ruwan turaren wuta a gefenta, aka shafa mata manshanu a fata, aka ɗinke mata zani da riga mai alamar Fulani na gargajiya—jar zani mai adon ratsi da santali na tsaf.

An saka ta cikin wani ɗaki mai ƙyalli da kilishi, ana yayyafa mata ƙamshi da bakhour, ana duba fatarta da gashinta, yarinyar ce kyakkyawa da kyau na halitta, ba ado ke ƙawata ta ba—rashin yawan maganganu da nutsuwar ta ce abin kallo.

A gaban limamin ƙauye da shaidu, aka daura auren Halima da Alhaji Saminu da sadaki naira dubu ɗari biyar, da sarkar zinari da kayan gida., adaidai lokacin da aka furta "na ɗaura", Halima ta fashe da kuka mai ƙarfi. Sai dai ba kuka na soyayya ko jin daɗin aure ba ne—kuka ne na rabuwa da matar mahaifinta, wacce ta raineta tun rasuwar mahaifiyarta, wani kuzarin tunani ya cika ta, kamar tana jin kamar yanzu rayuwarta ta sauya daga yarinya zuwa amarya, daga ƙauye zuwa birni.

Moddibbo ya share hawayen sa da alwala, yana murmushi mai cike da damuwa, yana fatan Halima zata dace da sabon rayuwar da zata tafi ciki, a zuciyarsa yana fatan Alhaji Saminu zai rike ta fiye da yadda aka rike 'yar sarki.

Alhaji Saminu ya bar ƙauyen ba da hannu ba. Ya bar da ɗimbin kyaututtuka: kudi ga matan unguwa, jakunkunan shinkafa, kayan abinci, sabbin riguna da ɗinkin zamani ga matasa, har da jakunkuna ga yara da aka ce "na makaranta".

Wajen fitarsu, aka shigo da sabuwar amarya cikin sabuwar rigar aso-ebi da kwalliyar santali, aka ɗaura mata gyale mai nauyin zinariya, aka raka ta da kalangu da wake-wake, aka saka ta cikin motar farin Lexus, sai ga kafila ta nufi birnin Abuja.

Amarya ta fito daga ƙauye—amma fuskarta na cike da tambayoyi. Shin me birnin ke ɓoye mata? Me Alhaji Saminu zai kasance gareta? shin wannan aure zai fassara soyayya ne, ko wata kyauta ta biyayya ce da ba zata taɓa jin daɗin ta ba?

********************************

Juyawa tayi da ƙarfi kamar wadda aka hangi zuciyarta ta nitse cikin ruwan kogin ɓacin rai. tana mai huci da numfashi mai nauyi, ta faɗa jikin Moddibbo kamar jaririya, ta rungume shi da ƙarfi, tana kuka mai girgiza zuciya dukkan gangar jikinta na rawar jiki, murya na rawa kamar ana buɗe gidan hawaye a zuciya.

Moddibbo ya kama kanta yana bubbuga bayanta da hannunsa mai sanyi da tausayawa.
"Allah ya sa ki dace Halimatu," ya faɗa da wani murya da yafi shiru nauyi. "ki rike mutunci, ki tsaya da imani kiye koyar da mahaifiyar ke a fagen haƙuri zaki ci ribar zaman duniya ... rayuwa ce bata da tabbas."

Shi kansa idonsa cike da ruwa, kodayake zuciyarsa ta taɓu sosai—ya jima yana kallon Halima tamkar zinariyar sa wanda yanzu ya mika hannunsa ya mika ta ga duniya. ya mika al'amuranta ga wani mutum da ya fi shi daraja da kima, amma ba shi da tabbacin soyayya.

Bayan kuka da ban kwana mai cin rai, sai Halima ta shige cikin motar Alhaji Saminu da zuciyar da ba a iya fassara. Alhaji yana ƙoƙarin rarrashi da annuri, yana ƙyalƙyala dariya mai taushi yana faɗin:

"Amaryata kada ki damu, Abuja ba abin tsoro ba ne ke zauna lafiya, za ki ga alheri."
Halima bata ce komai ba ta fuskanci gilashin motar tana kallon ƙauyen su da ke raguwa a bayanta kamar mafarkin da ya ɓace. hannunta na cikin haɗaɗɗiyar rigarta, amma zuciyarta na cikin tsohon zanin ƙauyenta.

Motoci suka fice daga Gembò, suka fasa hanyoyi masu kura, suka dosa garin Yola inda jirgi zai tashi zuwa Abuja. Halima na zaune cikin mota, amma kamar a mafarki ta kasa kallon sabbin gine-gine da suka wuce su, kamar ba su da ma'ana gareta.

A lokacin da suka isa filin jirgi, an ce mata "Halimatu! Ki sauka ",ta sauka cikin rigima, tana kallon ƙasa kamar tana tsoron ƙasa ce zata buɗe ta haɗiye ta ba ta san me ake nufi da "ticket" ba ba ta san yadda ake biya ba yanzu ne Halima ke fara jin bambancin rayuwa, ta kasa cire takalmanta a wajen sakan na'ura, sai da ma'aikaciyar ta fara dariya ta ce:
"Yarinya! ba salla za ki ba wannan tsafta ne da dokar jirgi."
taji kunyarta sosai Idonta ya cika da ƙyama da tozarta a zuciyarta:
"kai! ashe akwai duniya kamar haka?"

Bayan an kaita cikin jirgin, aka ɗaure mata seat belt, ta riƙe kujerar kamar wacce ke cikin ruwa

mai zurfi. Da jirgi ya tashi, ta saki ƙara mai firgitarwa:
“Innalillahi wa inna ilaihi raji’un! Wayyo Moddibbo…! na mutu!”
Alhaji Saminu ya rike hannunta da dariya “babu komai Halimatu, jirgi ne ke tashi kawai.”

Kamar sabuwar tsuntsuwa aka ɗauke daga ciyawa, aka ajiye cikin gini mai fanfo. As zuciyarta, birni kamar wata. Amma tambaya ɗaya ke ci mata rai: Shin wannan sabon garin da take ciki zai taimake ta ta samu sabuwar rayuwa, ko zai ɓata mata tunanin da take tsaye da shi tun ƙuruciya?

Tunda suka hau cikin jirgin sama, Halima ta kasa zaman lafiya idanunta na zagaye cikin hadadden komai wanda ba ta taɓa mafarkin wanzuwarsa ba , tana kallon tagar gefe, tana ganin sararin samaniya da ƙasa na raguwa kamar yadda aka rage wa tunaninta hankali. amma wani abu ya sake ɗaukar mata hankali...

A kujerar bayan nata, wani saurayi ne zaune, ya murtuƙe fuska, idonsa kamar na damisa mai zurfin tunani , fuskar sa doguwa ce, fara tas kamar bulo, ƙuncinsa yana da ɗan launin ja, bakinsa siriri ne amma mai ɗan ƙasaita  gashin kansa an rage shi tsaf yana sheƙi, sai karan agogon zinare a hannunsa na hagu ya ƙara ɗaukar hankali.

Shima yana kallon Halima, ba da sha’awa ba, amma da mamaki da tausayi kadan kamar yana cewa da kansa, “Ina aka samo irin wannan ‘yar ƙauye mai tarin kamala?”
suna cikin tashi ne Halima ta saki ihun da ya gigita kowa
“Wayyo Allah naaa! waye ya ce jirgi zai ɗaga?! Innalillahi wa inna ilaihi raji’un!”

Mutane sun juya suna kallonta, mata suka dinga dariya a nutse, wasu kuma suka tausaya amma shi saurayin da ke baya—ya kalli fuskarta da jajayen idanu, yana juyar da kansa a hankali cikin murmushin gefen baki, kamar wanda ya saba da irin haka a rayuwar zuciyarsa , sun sauka a filin jirgin Abuja, wanda ya bude musu sabon shafi a rayuwa.

Alhaji Saminu ya nufi Maitama da su, inda katafaren gidansa ke cike da girma da kima. gidan na da kofa babba mai lanƙwasa kamar ƙofar masallaci a Makka. farfajiya ce a waje, da lambu mai yalwa, sai tsuntsaye ke ta raira waka kamar sun san sabon baƙuwa ta iso.

Yayin da Halima ta kalli ƙofar katafaren gidan, zuciyarta na wani irin doki da tsoro da fargaba, wani sashe na ruhinta na faɗin "kin fito daga ƙauye, amma an jefa ki cikin birnin masu hannu da shuni..." da zuciya ɗaya ta shiga, sanye da kayan aure na gargajiya: mayafin fulawa, zobba a yatsu, da dankwali mai yatsin zinariya.

A cikin gida, motoci sun sha jerin gado, masu gadin gidan biyu a ƙofar shigowa suna miƙa gaisuwa da ban girma. Gidan kuwa – katafaren alfarma ne wanda ba a taɓa mafarkin Halima zata taka kafarta ciki ba. Babban falon yana da manyan tagogi masu labulen fata na turkiyya, cike da fitilu na chandelier masu hasken zinariya, cikin falon ne Hajiyah Nafisa ta karɓe ta da murya mai cike da mamaki:

Matar Alhaji Saminu, Hajiyah Nafisa, ta fito sanye da kayan alfarma gashinta a jikin mayafi yana sheƙi kamar rigar sarauta ta kalli Halima da murmushi na ɗan lokacin, amma idanunta na cike da alamun tambaya:
"Itace wannan yarinyar?"
Halima ta kasa magana ganin palon gida kadai ya isheta tiles ne na zinariya da hoda mai sheƙi, fanfo a bango da tebur na gilashi. tana takawa kamar ana binsa da ƙasa. Zuciyarta na cewa:
"To wallahi... haka birni yake ko dai na mutu ne an kawo ne gidan aljanna ?" kwalliyar da aka yi mata da kayan Fulani na auren ƙauye—maye da zobe da mayafi na fulawa—ya sa ta ƙara haske , amma a fuska akwai shakku, akwai salo na "ba sani ba sabo." sai dai akwai mutunci a tafiyarta, wanda ba'a koya shi a birni.
"Nafisa itta ce amaryata na biya sadakinta tun can ƙauye kamar yadda na gaya miki. Allah yasa alkhairi."
Hajiyah Nafisa ta tabe baki cikin murmushi mai nauyin fahimta daga kallon ta ɗaya ka gane ko da tana ƙoƙarin karɓarta, zuciyarta ba ta cikin hakan gaba ɗaya.

Sai da aka kai ta ɗakinta da aka tanadar mata cikin gida   ɗaki mai faɗi sosai, bangon sa mai launin cream da zinariya an shimfiɗa masa carpet mai laushi, akwai gado babba da labule mai juyawa kamar na sarauta taga biyu na dakin suna kallon lambun cikin gida, inda tsuntsaye ke ta shawagi, cike da kyan gani. dakin na da fanka da AC, amma Halima bata san amfani da komai ba. Sai kallon su take kamar kayan sihiri.

Ta zauna a gefen gado daidai lokacin wata mai aiki – Hasiya – ta shigo da murmushi a fuskarta. Hasiya daga Sokoto ce, mai ƙanƙantar jiki da zubin kawaici atake suka fara haɗuwa Hasiya ta ce da ita:
"Wallahi  Aunty Halima kin yi kyau, da gaske ne ke daga ƙauye?"
"Eh... daga Gembo," ta ce da dariya mai daɗin ji. "kin taɓa jin sunan kauyen?"
 "A'a, amma yanzu na ji ki. sai dai ki gyara nan Abuja fa ne Idan baki yi wayo ba, sai a cuce ki."

Nan suka fara zama ƙawayen gaske. Halima ta fara ɗan sabawa cikin gidan, musamman da yaran Alhaji Saminu goma da ke gidan. akwai Muneerah da Ruqayyah – 'yan mata manya masu haɗe da kwalliya da rashin kunya, masu jin turanci da yi wa Halima kallon kamar uwar kauye suna kiran ta "that girl from bush" a bayan ta.

Sannan akwai Aminu Junior da Zaid, samari matasa da suka fi ɗaukar lokaci a wajen gidan basu  damu da sabuwar mace, sun fi shagaltuwa da motocinsu da rayuwar club da Instagram.

Yara uku ƙanana—Sulaiman, Abbas, da Fadilasun fi sabawa da Halima suna zuwa ɗakinta suna wasa da ita  ta dinga yi musu wasan shanu da dabbobi da kida da rawa irin na ƙauye, suna dariya kamar an saka musu annashuwa a zuciya  tana ɓoye wannan zumunci da su domin kada uwayensu su ji.

Matar biyu kuwa, Hajiyah Mariyah da Hajiyah Sabeerah, su ne abokan huldar Nafisa amma Hajiyah Mariyah ce shaidaniya, mai haƙurin fitina da halin mugunta tana kallon Halima da

kyankyami, tana cewa:
“Wato wannan ƙaramar ‘yar Fulani ce ta zo mana da daddare? Allah ya sa ba za ta ja mana Alhaji ba.”

Tun daga rana ta fara tsara yadda zata nunawa Halima cewa gidan ba da sauki ba ne. tana tura mata ayyuka kamar ba matar aure ba: “ki share wancan, ki gyara kicin, ki tafi can ki goge banɗaki.”

Halima kuwa, da jin kunyar Fulani da biyayya, sai ta dinga yi tana mika hannu da zuciya, ba tare da kuka ko korafi ba inda Hasiya ta fi shiga tsakiya, tana mata nasiha da rarrashi:
“Ki yi haƙuri Halima, nan ne birni idan kika nuna rashin juriya, sai su hana ki kwanciyar hankali amma Allah yana tare da mai gaskiya.”

A haka Hajiyah Nafisa ta dinga kallon yadda Halima ke yi wa yara wasa, tana girki da kyau, tana wanke-wanke da murmushi da farko tana kyamar ta, amma wata rana ta shigo dakin Halima sai ta ganta tana dinki wa Fadila riga da hannu wani abu ya motsa a zuciyarta. Ta ce da kanta:
“Wannan yarinyar... ba ta da mugunta kuma girmanta yana shigowa hankali.”

Halima kuwa har yanzu bata san haka ba. zuciyarta na yawo ne da tambayoyi: “shin wannan rayuwar ita ce rabona? ina mahaifina da mahaifiyata? W
wannan Alhaji Saminu fa, me yasa yake sona?
wani dalili ne yasa ya kawo ne gidan sa ya ajiye tsawon lokaci bai dawo garine ba?

Ohhhhhhhh ga Halima ga Abuja
a sannu a hankali zamu shiga labarin Halima

continued ƙanwar soja in Sha Allah

✍️

https://chat.whatsapp.com/BsQ0CkOCA83FgwnQ177z9y

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON🌕

BY
NARNAH KANWAR SOJA
MARUBUCIYAR
MIJIN MAGE
FARASHIN SO
BIYAYYA GA UWA
DUHU CIKIN HASKE
RUHI BIYU
HANYAR RUWA
MAI CIKI CE
MADOBIN IDO
AHLIN LASHKAR
PRINCESSS RAHILAT
RAYUWAR UMMAH
BAYAN WATA

💫ROYAL STAR WRITTER'S ASSOCIATION 💫

SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star

Wannan page na sadaukar dashi ga mutum biyu Sister Juwairiyya M Lawan tare da Najeeb Allah ya bar zumunci enjoy the page guys

Wata bakwai kenan cif da zuwan Halima gidan Alhaji Saminu wata uku na rayuwa da ke cike da shiru, da sanyi, da kewa, da dogon kallo zuwa fitilun falon cikin dar wata bakwai bata taɓa ganin fuskar mijinta ba sai sau biyu kacal sau na farko da ya kawo ta gida, na biyu kuwa yana wucewa da mota, ya tsaya da taga yana kallon ta ba tare da ya sauka ba.

Tunda lokacin, Halima ta fara tantama: “shin ni matar aure ce ko kuwa ba haka bane? ko kuma na fi zama ‘yar aikin gidan alfarma da ba ta san ko wane ne mijinta ba?”

Gidan kuwa kamar gida ne na almara: bangarori fiye da shida, kowane ɗaki kamar wani gida daban. Halima ko bandakin da aka ce na nata ne ma sai da Hasiya ta koya mata hanyarsa da yadda za ta kunna ruwa daga famfon lantarki ta ƙi fita daga dakin nata sai idan da gangan, yaran gidan sun zama mafita ga zuciyarta Sulaiman da Fadila na mata wasa, suna biye mata da dariya da kida da rawar kauye ita kuma tana jin daɗin hakan, tana samun nishadi duk da zuciyarta na ci gaba da yin rauni da damuwa.
a wannan daren, kamar kullum, ta zauna a dakin nata cikin sanyi mai daɗi daga AC da fitilar tagwayen da ke ba dakin ƙamshi ta jingina da kujera, tana kallon hoton kwane-kwane da aka ɗora a bango hoton tsaunuka da furen da bata taɓa gani da ido ba, hawaye ya fara gangaro mata ta shafa su da gefen zane, tana kiran zuciyarta da sunan gida: “Kauna, Kaka, Baraka... ina kuke? ko na fice a nan in dawo Gembo da ƙafa ne? ko gidan da kuke tsirfa hatsi yanzu, ko na fi wannan?”

Daga nan, bacci ya ɗauketa cikin sanyin dare mai ɓoye zuciya cikin mafarki, Halima ta tsinci kanta a kusa da wani tafki mai ruwan shudi gabar tafkin akwai ciyayi masu launin zinariya, tsuntsaye na waka, iska na busa kamar karamar waka, ta tsaya cikin tufafin fararen zinariya, kanta a rufe da mayafin rawaya , can gefe kuwa, wani saurayi na kallon ta tsayuwarsa mai ƙayatarwa ce: dogo, baƙi, yana sanye da farin riga da wando. amma fuskar sa dukk ta ɓoye a inuwa kamar fuskarsa na ɓoye da nufin ya dawo wata rana.
“Halima...” muryarsa mai sanyi, mai kaɗa, tana ratsawa har cikin jijiyoyinta.“kai wa kake ne?” ta tambaya da muryar yarinya. “kayi kama da wani na kusa da zuciyata...”
“Ni ne mai zuciyar da ta kira ki cikin bacci... da zuciyar da zata so ki fiye da yadda kike so kanki.” ya miƙa mata hannu, amma kafin ta kamo ta farka tashi da sauri, numfashinta ya kadu, zuciyarta na bugu tana kallo sama kamar zata gan shi a cikin silin.
“waye wannan? me yasa mafarkin nan ya shige ni haka? Kuma me yasa fuskar sa ta ɓoye kamar akwai abu da ba a shirya bani ba?” karo na farko tun da ta zo birni, Halima ta fara jin wani abu daban – kamar mafarkin soyayya da sabuwar rayuwa na faɗa mata, "akwai wani sirri da ke tafe... kuma akwai wanda zai sauya maki rayuwa, ko da ba yanzu ba."

Kullum cikin dare, Halima na ƙoƙarin rubuta abubuwan da ke faruwa da ita a cikin wani ƙaramar littafi da ta ɓoye cikin almara ,tana rubuta mafarkinta, ƙiyayyar Hajiya Mariya, da muradinta na ganin wata rana zata fita daga gidan nan cikin daraja.
“Ina mafarkin wata rana zan fita daga nan ba da hawaye ba, sai da murmushi kuma duk wanda ya raina ni, zai ga matsayi na kuma wanda ya tsare zuciyarsa a gareni, zai gane cewa ba wai 'yar kauye bace, sai dai baiwar Allah da daraja ta ɓoye.”

*****************"""""

Abdullahi Khalil Usman wanda da dama ke kira Mr. Abdullahi, shine shugaban babban kamfanin gado na mahaifinsa wanda aka sani da Usman Holdings International, wanda hedikwatarsa ke cikin Abuja, amma reshe-reshen sa sun watsu a duk fadin Najeriya da kasashen waje duk da wannan girman arziki, Abdullahi mutum ne mai natsuwa, mai son zaman shiru, kuma yana da ɗabi’ar kin yarda da auren dole.
“Ni bana son aure yanzu. Ina jiran yarinyar da zuciyata zata karɓa ba tare da tilas ba,” inji shi kullum idan mahaifiyarsa Hajiya Binta ta taso masa da lamarin aure.

Tun yana ɗan shekara ashirin da shida, Abdullahi ke yin wani irin mafarki na wata budurwa mai kamun kai, mai kyan hali, cike da nutsuwa , kullum fuskar yarinyar bata bayyana gaba ɗaya, sai murmushin ta da kuma yadda take tafiya cikin kwanciyar hankali kamar ba ta san duniya ba.

Yanzu yana da shekara talatin da ɗaya, amma har yanzu bai manta wannan mafarkin ba har ya kasa yarda da kowacce mace – saboda zuciyarsa tana jiran wannan mafarkiyar da bata bayyana ba.

Ranar da ya hau jirgin daga Yola  zuwa Abuja, yana tsaye yana shan iska da kallon mutane, sai idonsa ya sauka akan wata yarinya da ke tafiya da Alhaji Saminu – cikin riga da zani, fuskar ta cike da tsantsar kauyanci da kamun kai. Fuskar yarinyar kamar dai fuskar yarinyar mafarkinsa ce! amma sai ya girgiza kansa:
 "A'a, ba zata iya zama ita ba… ai ita kauyaniya ce ko  turanci ma bata iya ba." ya fad'a a ransa, yana danne mamakin zuciyarsa amma tun daga lokacin, idonsa na bibiyar Halima, duk da cewa bai san sunanta ba, kuma bai ce da ita uffan ba. Sai dai a zuciyarsa… ya kamu da wata ƙayatarwa mai cike da ban mamaki.

Yanzu da suka sauka Abuja, Abdullahi ya koma rayuwarsa, amma zuciyarsa bata daina tunanin Halima ba duk wata yarinya da ya gani, sai ya kwatanta ta da ita, amma babu mai dacewa shi kuwa Alhaji Saminu, yana cikin shirye-shiryen cin gajiyar auren Halima – yana kula da ita da nisa, amma bata san yaushe zai dawo ba Halima kuwa, tana fama da azabar rayuwa a gidan kishiyoyi, tana ta mafarkin sauyi da ƙauna, amma bata san cewar zuciyar wani saurayi mai daraja tana neman nata ba

Abuja   cibiyar kasuwanci da masarauta ta zamani wannan karon, babban taro ne da ya haɗa manyan kamfanoni, 'yan kasuwa, da shugabannin kasashen duniya  Alhaji Saminu, wanda ya kafa taron kasuwanci, yana cikin wani kwararren d'akin taro a babban otel na Abuja, wanda ke dauke da kyan gani da yanayi mai cike da alfarma duk duniya na kallon wannan taro da alamar samun ci gaba ga kasuwancin Najeriya manya da ƙananan kamfanoni sun hada kai domin samun nasara da bunkasa tattalin arzikin kasar.

A cikin wannan dakin, Abdullahi ya tsaya cikin cikakken kwalliya jikin sa yana ɗauke da rigar alfarma mai kyau, wanda ta haɗa da jallabiyah mai launin zinariya da farar rawani fuskar sa tana cike da kyan gani da kwarjini. Duk wanda ya kalli shi zai fahimci cewa yana ɗan kasuwa ne mai daraja, wanda ke dakin taro ba domin wasa ba a cikin zuciyar sa akwai fata na samun nasara mai girma, amma akwai wata yarinya da ta mamaye zuciyar sa – Halima.

Abdullahi, wanda iyayensa ke son shi ya auri wata mai matsayi daga cikin iyalai masu arziki, yana neman neman soyayya ta gaskiya. bai taɓa ganin wannan soyayya ba a cikin kowanne daga cikin yarinyoyin da iyayensa suka so masa amma a cikin zuciyar sa yana ɗokin haduwa da Halima, wanda ya ga a cikin mafarkinsa a jirgin sama lokacin da suka haɗu tabbas yanzu zuciyarsa yafi karkata ga cewa ya haɗu da mafarkin sa a rashin lura irin  tasa .

A yayin da aka gudanar da taron, Halima tana cikin wani dakin hotel ɗin da Alhaji Saminu ya shirya mata wannan d'akin yana ɗauke da kayan alfarma da kyakkyawar kwalliya – gado mai kyau da tsayayyen fata na zinariya. Halima ta zauna cikin dakin, tana kallon kayan da aka tanadar mata, amma zuciyar ta cike take da tunani wataƙila, wani abu ya faru da ta rasa kwarin gwiwarta, ko kuwa har yanzu tana jin cewa wannan ba shi ne rayuwar da ta yi mafarki da ita ba.

Alhaji Saminu ba ya kula da wannan sha'awar da ta ke nunawa  a saboda haka, yana son ta zama abokiyar rayuwarsa, amma yana ɗaukar ta a matsayin daya daga cikin matan da zai kula da ita daga ɓangaren kyakkyawar tarbiyya da kuma halayen aure.

A cikin taron kasuwancin, Abdullahi na cikin dakin taro, yana kallon yadda ake gudanar da al'amuran. A zuciyar sa, yana jin cewa ba zai taɓa samun zaman lafiya ba sai ya sadu da Halima. ya tuna da fuskarta a cikin jirgin sama, da yadda zuciyarsa ta shiga cikin hayaniya saboda soyayyar da ta shige masa cikin zuciya ,yana ganin ta a cikin wannan dakin, amma ba

zai iya neman ta yanzu ba. wannan tsari na al'amura yana nuna masa cewa soyayya ba ta da sauki, kuma yana bukatar lokaci don samun damar yin matakin da ya dace.
Tsawon kwanaki biyu ana wanan gagarumin meeting nin inda ake shirye shirye rufe taron a kwana na ukku Alhaji saminu dalilin ɗauko Halima daga gida bayan kumawae sa gida cikin gaggawar kirar taron da suke gabatar wa yanzu cikin bazata ya iso gidan ganin halin da Halimar ke ciki ne ya bashi mamaki kwarai da gaske wannan dalilin yasa ya ɗauko ta a tare dashi ....

RANAR TARON ƘARSHE

Ɗakin taron babban hotel ɗin na Abuja ya cika da hasken chandelier mai sheƙi kamar taurari fata-fatan zinariya da tabarmar da ta shimfiɗu kasan tiles ɗin falo suna haskakawa da salo irin na manyan duniya.

An shimfiɗa dogon babban tebur na gilashi, aka jera kujeru masu launin royal blue da zinariya agefen teburin akwai lambun furanni masu ƙamshi, da sauran kayan kyauta na kamfanoni. mutane masu siriri da sirarrun suits sun cika gurin: 'yan kasuwa, manyan 'yan banki, masu hannun jari, da CEOs daga kamfanoni daban-daban.

Abdullahi, sanye da suit mai launin baki da farin riga da blue tie, ya zauna a tsakiyar babban kujerarsa girman sa da kamewar sa ya ja hankalin kowa — da kallo daya zaka san ba na yau aka haife shi ba fuskar sa ba dariya, ba kuma fushi  tsaka-tsakin kamewa da matsayi Hausawa sukace yaro da kuɗi abokin tafiyar manya

Har lokacin da Alhaji Saminu ya shigo cikin taron, aka mika masa gaisuwa irin ta manyan masu kuɗi ya zauna da kamun kai, yana ta gyaran hula da hancinsa lokaci-lokaci, alamar rashin jin daɗin zama saboda tunanin a maryar sa , lolz

A takaice an yi taron a cike da muhimman magana: aka rattaba hannu akan sabon kwangilar gine-gine da haɗin gwiwa bayan an gama taron, mutane suka shiga gefe suna ta yin hotuna,

musabaha da exchange card.

A gefe kuma, Halima wacce aka bar a dakin hotel na VIP floor, tana kwance tana ƙoƙarin danne kukan kewar gida da tsoron birni.
tana sanye da kayan gida masu kyau amma ƙauyanci ke bayyana sosai a fuskarta  Fuskarta bata da kwalliya, sai ruwan hawayen da ta share, tana kallon window tana ganin duhun dare yana sauka kan manyan titunan Abuja.

bayan taron, Alhaji Saminu cikin gaggawa ya amsa kira daga gida  an kira shi da sauri, wani ɗan matsala ce ta dangi da gaggawa ya fice daga hotel ɗin... amma sai ya manta da Halima a cikin ɗakin hotel ɗin!

Halima tana jiran shigowar sa, tana jin tsoron shiru da tunanin abubuwa daban daban
Halima ta jawo ƙofar ɗakin a hankali, tana hango hanyoyi masu haske da furen bango. tana sanye da doguwar riga mai launin shudi mai launin ruwan sama, wanda ke fita da kyau akan fara fatarta, tana tafe da ɗan ƙaramar gyale mai launin milk da ya ɗaura mata fuskarta kamar an kare ‘yar Sarki.

Tsoron da ya mamaye ta ya hana ta saka takalma — tana tafiya a siraran ƙafarta, tana kallon dukkan gefuna da tausasan idonta.
tana jin kowane sauti kamar wani abu zai fito daga cikin duhun corridors ɗin hotel ɗin.
ta isa ga wani ɓangare na babban hotel ɗin gaban lift — lokacin da abinda ta gani ya firgita ta.

Da gudu ta nufi cikin tsoro tana neman mafaka — gaban ta a bude — tayi karo da mutum mai tsayi, sanye da baƙin suit mai sheƙi, riga fara ta ciki, wanda ba kowa bane illa Abdullahi.

Shi kuma yana tsaye yana danna wayarsa, iska mai sanyin ƙanshi na air conditioner yana kadawa a gashinsa mai santsi.zuciyarsa tana bugawa da sauri kamar ana gaggauta dokin sarauta,  Halima cikin firgici ta fado jikin Abdullahi — hannuwanta suka kama rigarsa, tana fitar da ƙaramar ajiyar zuciya, idanun su suka haɗu ,wani zafi mai daɗi ya ratsa tsakanin su, wani sirrin shiru mai nauyi ya cika sararin tsakanin su.
wayar sa ta tsaya hannu, zuciyarsa ta kasa ci gaba da bugawa daidai Idonta ya cika da tsoro, nashi kuma da wani irin salo na jin "na gan ki amma ban gane ki ba".

A hankali Abdullahi ya daidaita kansa, yana ƙoƙarin saukewa Halima daga jikinsa.
Ya sauke ta a hankali kamar kar ya tsoratata, sai ya ɗauke numfashi ya runtse ido tsakanin su shiru ne mai nauyi, kamar ana iya jin karar fitar numfashin juna.
Abdullahi ya tsaya wuri guda, idanuwansa suna zurfafa cikin kyawawan idon Halima waɗanda ke cike da tsoro da rashin tabbas cikin kin sauti mai kaɗan amma cike da girma da tsari, anji muryar Receptionist "Please, Hajiya Halima...! Reception is calling you, Hajiya Halima!"

Muryar ya sake maimaitawa daga speaker din da ke jikin bango, kamar an daga karar.
Halima ta ji sunanta a sarari, kamar daga sama, kamar ruwa an zuba mata ,wani sabon firgici ne ya sake ratsa ta kamar numfashin ta zai tsaya a firgice, ta sake matse jikinta da ƙarfi a cikin ƙirjin Abdullahi, tana neman mafaka daga kowa da komai ,Abdullahi kuwa ya saki wayarsa ta faɗi ƙasa ya kasa motsi.
Numfashin sa ya tsaya cak
gaba ɗaya jikinsa ya birkice kamar karamin yaro da aka tsorata masa da aljani.

A hankali yana jin kamshin furen Halima — kamshin shinkafar ɗanye da ƙamshin turaren wuta idonsa ya lumshe, zuciyarsa na harbawa da irin bugun da bai taɓa ji ba a rayuwarsa.
ya buɗe idonsa, ya kura mata ido, yana kallo cikin fuskarta mai tsantsar kyau da rashin fenti fatar ta laushi tamkar auduga, launin idonta kamar kalar ruwa mai tsafta

Bakin Halima ya motsa kaɗan, tamkar zata ce wani abu, amma ta kasa.
Abdullahi ya bi bakin nata da kallon da ya kashe masa nutsuwa — laɓɓanta sun yi ja kamar sabuwar ɗan itacen ɗinya, santsi da kauri irin na 'yar asali.

Abdullahi ya shige duhu da hasken idonta.
wani abu mai daɗi da tsoro na haɗuwa ya cika shi abu da bai taɓa jin sa ba tun daga haihuwarsa " tabbas ittace mafarki na ".
Abdullahi ya kasa inda zai sa kansa.
Zuciyarsa tmkar an kunna ganguna.
wani yanki na zuciyarsa na ba shi shawarar ta hanyar hankali: "ka sauke ta, ka da ka zalunce ta!"
Amma wani sashe kuma, na tunani mai zurfi da sha'awar kasancewa tare da ita a dau dai wannan lokacin yana fisgarsa tamkar walkiya:

Wani numfashi mai nauyi ya saki — yana jin tamkar zuciyarsa zata fashe da nauyin soyayya da radadin rashin tabbas.
idanunsa suka kai ga fuskarta.

Daidai lokacin da yake shirin sauke wata ƙaramar ajiyar zuciya, sai suka ji motsi da sautin takalmi mai nauyi,
Alhaji Saminu ne ya shiga  jikin sa akwai alamar gajiya da fushi, yana janye zuciyarsa da sauri daga tunanin da take shirin narke shi.

Alhaji Saminu ya tsaya cak, yana kallon yadda Halima ke manne da wani saurayi, shi kuma saurayin kamar an soka masa gashin zuma a ƙirji fuskarsa ya cika da shakku da mamaki.
Yayi wani takun ɗan girma da iko, ya nufo su.

Abdullahi ya gano hakan cikin kwana na biyu na idon sa ,ya ja hannun Halima da sauri, cikin ladabi da nutsuwa, suka tafi daga wurin.

Halima kuwa, tana kallon Abdullahi tana kuka mai sanyi, hawaye na bin fuskarta tamkar silin ƙwai da ya fashe a hankali.
bata so a raba su bata so a bar wannan ɗan lokaci ya wuce ba.

Har lokacin da suka rabu, Halima na ta juyawa tana kallonsa cikin raɗaɗin zuciya — kamar tana jin cewa ba za su ƙara saduwa ba, tana maimaita sunan sa a zuciyar ta da jaddada cewa tabbas shine a mafarkin ta ,
shi kuma Abdullahi, da yatsun sa guda huɗu ya shafi labbansa a hankali yana jin ɗumin halittarta har yanzu a jikin sa, yana binta da kallo tamkar yana so ya hango sirrin da bai bayyana ba.

Duniya ta yi wa zuciyoyinsu nauyi
wani sanyi da rashin lafiya na musamman ya mamaye Abdullahi, zuciyarsa na fuskantar wani

sabon yanayi da bai saba da shi ba.

Halima ta kasa daure hawaye tana cikin ɗa
Abdullahi ya tsaya cak yana kallonta, zuciyarsa na bugawa da ƙarfi, amma ya tilasta kansa ya sake ta ta tafi da Alhaji Saminu.
aguje zuciya, yana ji tamkar an sare wani ɓangare na ruhinsa.
yana kallon bayanta har ta ɓace a cikin motar , ya runtse idanu cike da damuwa, numfashi mai nauyi ya suɓuce daga bakinsa.

Da zarar Alhaji Saminu ya dawo, ya zube a babban kujerar falo yana huci.
wani irin kishi ne da fushi ya turnuƙa masa zuciya  har yana jin idanuwan sa na sauya launi
Hajiya Nafisa da sauran matansa suka taru suna kallon sa cikin mamaki da tausayi, amma basu isa su tambaye shi komai ba.

Ya ɗauki kofin shayi dake gabansa, ya buga da ƙarfi a ƙasa, kofin ya tarwatse.
yara suka firfito daga ɗakunan su suna kallon sa cikin tsoro
Halima kuwa, tana zaune a bayan kofa , tana kokarin hana hawaye kwarara daga idanuwan ta tana jin tamkar wata sabuwar ƙaddara ce ke shirin saukar mata.
a wannan daren, gidan ya cika da nauyin shiru da hayaniyar zuciyoyi   shiru mai ɗauke da kishi, da ƙyalle-ƙyallen wani mugun fushi da za a sake fallasa a kan Halima…

https://chat.whatsapp.com/BsQ0CkOCA83FgwnQ177z9y

🌗🌙BAYAN WATA🌙🌗
AFTER THE MOON🌕

BY
NARNAH KANWAR SOJA
MARUBUCIYAR
MIJIN MAGE
FARASHIN SO
BIYAYYA GA UWA
DUHU CIKIN HASKE
RUHI BIYU
HANYAR RUWA
MAI CIKI CE
MADOBIN IDO
AHLIN LASHKAR
PRINCESSS RAHILAT
RAYUWAR UMMAH
BAYAN WATA

💫ROYAL STAR WRITTER'S ASSOCIATION 💫

SADAUKARWA
Wanan littafin sadaukarwa ne a gunke gaba-daya ta bisa jajjircewa da bajinta a duniyar mu na marubuta Allah ya taimaka ya kara basira da hazaƙa gaba gaba sister 💕
Zahrah Royal Star



Bayan Shekaru Biyu

Tunda ranar da suka rabu a babban ɗakin taron hotel ɗin Abuja, Halima da Abdullahi basu ƙara ganin juna ba. kamar dai wata fata da iska ta ɗauka ta ɓoye a doron ƙasa, haka soyayyar da suka ambato da shiru a idanuwansu ta ɓuya cikin zuciyarsu duk da lokaci ya shude, rana ta fito ta fadi sau dubbai, a zuciyarsu har yanzu tamkar jiya aka faru.

Abdullahi, da zarar ya koma gida, ya shiga tashin hankali mai tsanani mafarkin Halima, kallo daya da ya yi mata, da sautin murya da numfashinta, suka mamaye dukkan tunaninsa duk da irin dattijon haiba da ƙwazo da yake da shi, ya zama tamkar yaro a duniyar soyayya. ya yi iya ƙoƙarinsa ya guje mata, ya ɓoye a cikin aikin sa da tafiyar kasuwanci, amma zuciyarsa ta ƙi amincewa da sabuwar rayuwa har dai iyayensa suka matsa, suka zaɓa masa matar aure daga cikin manyan iyalan su, suka lallaɓa zuciyarsa da hujjar cewa "ba a dukan soyayya ake rayuwa ba."

Da damuwa da karyewar zuciya, Abdullahi ya karɓi zabin iyayensa amma a zuciyarsa ya san: soyayya ta gaskiya daya tal ce kuma Halima ce yayi aure a matsayin ɗan biyayya, ba a matsayin ɗan farin ciki , bayan ya tabbatar da cewa Halima mata ce a gidan Alhaji Saminu.

A bangaren Halima kuwa, rayuwarta da Alhaji Saminu ta fara dusashewa da kwanciyar aure. Alhaji Saminu bai sake kallonta da idon da ya saba da shi ba tun ranar da ya ga yadda ta rungume wani saurayi a hotel kullum yana ganin tamkar ta kai girma da zata saki jiki da wani ko da kuwa ba laifinta bane, ko da kuwa ransa ya tabbatar cewa tsoro da ruɗani ne suka jefa ta.

Auren Halima ya koma tamkar ɗakin sarauta mai cike da shiru da fargaba matansa na farko na ci gaba da wulakanta ta, musamman Hajiya Mariya, wacce kullum take ƙoƙarin ganin ta gaza Halima kuwa, tana rayuwa ne tsakanin kuka da shiru, tsakanin mafarkin soyayya da gaskiyar rayuwa kullum cikin tunanin cewa ƙaddara ce ta raba ta da masoyinta, kuma soyayyar da take jin daɗinta tun ƙarama ba zata cika ba har abada.

"Idan soyayya kaddara ce, to ni na riga na mallake ta, ko da da hawaye zan sha..." Halima na faɗa cikin zuciyarta a duk dare, yayin da take kwana tana duban sararin sama daga taga mai ɗimbin ƙawatawa, amma mara 'yanci.

Rayuwa ta ci gaba da tafiya...
sai dai zuciyoyin masoya biyu suna ci gaba da harbar juna da addu'a cikin nisa, cikin rashin sani ko Allah zai kawo wata rana su haɗu ko kuwa soyayyar su zata kasance soyayyar da bata da makoma?
duk da wulakanci da mugun hali da Halima ke fuskanta a gidan Alhaji Saminu, zuciyarta ta ki rabuwa da sunan Abdullahi.
Abdullahi — wanda tun ranar da suka haɗu a hotel din, zuciyarta ta tabbatar da cewa shine mafitar rayuwarta.
duk daren da ta kwanta cikin kuka da zubar da hawaye, da ƙaunar da take shirin fashe mata ƙirji, sai ta runtse ido tana kiran sunansa da shiru.
"Abdullahi... kai ne mafita ta... amma ka riga ka zama mafarki..."
ko da cikin jikinta yana girma, bata daina jin ƙaunar Abdullahi ba. Sai ma ƙara shigewa da ƙara jin saukin duk wani raɗaɗi idan ta ambaci sunansa a ranta.

Amma fa duniya bata tsaya jira ba,rayuwa ta cigaba da danne ta a karkashin ƙafa, har ta kai ga lokacin haihuwa ya kure.
ranakun karshe da suka rage mata a duniya, wahala ta fi karfin bakinta cikin da ta ɗauka cikin ciwo da azaba ya girma har ta cika da tsoro da fargaba ba wanda ke kula da ita
ba wanda ke tambayarta lafiya ko da take ciwo dare da rana, sai Alhaji Saminu ya ce da ita "ke kanki kika ja wa kanki, na gaji da wannan kuka da ciwo ."
ba komai ya jawo hakan ba sai sanin cewa tsantsan soyayyar da takewa wani alhali tana da nata auren
A karshe, ranar da komai ya ƙare

ranar da zatai haihuwa  Halima ta shiga wani ciwo da ba a iya kwatantawa, Alhaji na chan hotel yana meeting bai ma san cewa Qatar haihuwar ta ya kama ba.
A kwance a ɗakin da aka ajiye ta cikin wulakanci, ba likita, ba uwargida, ba taimako  sai kuka da ciwon da ke yawo daga ƙasan jikinta zuwa ƙirjinta yana neman karya ta.

Kuka take kamar zata fashe.
Tana kiran Baffa, tana kiran Abdullahi, tana neman taimako amma shiru!

Abdullahi a lokacin yana cikin wani babban business meeting, yana fuskantar matsin rayuwa sakamakon tarin matsaloli da ya dinga samu tun da ya yarda da zaɓin da iyayensa suka masa.
soyayya da Halima ta fara girma masa a zuciyarsa ba ta gushe ba, kullum yana mafarkin fuskar ta, murmushinta, da halayenta.
amma bai san halin da take ciki ba.
bai san tana shirin barin duniya ba.

A cikin tsananin raɗaɗin haihuwa, Halima ta ƙara ruɗewa, ta kurma ihu, ta kifa kanta a shimfiɗa tana ihu kamar rai na fita:

"Ya Allah... Abdullahi... Abdullahi... na yarda da ƙaddara..."inda yayi dai dai da shigowar Alhaji sakamakon korar Hajiya nafisa sai dai, kafin a kawo taimako, kafin a kawo likita halin ya lalace ,numfashinta ya fara yanke-yanke.
zuciyarta ta yi shiru.
Idonta ya tsaya a sama yana kallon wani abu da kowa baya gani, ahankali Halima ta kwantar da kanta gefe, ta saki numfashinta na ƙarshe da kalmar:
shahada , ta mutu.
ta mutu cikin radadin soyayya.
ta mutu cikin ciwon zubar da hawaye.
ta mutu ba tare da samun saukin zuciya ba.

Bayan rasuwar Halima...

Tunda aka sallaci Halima tare da jaririnta da bai samu damar saukar numfashi ba, gidan Alhaji Saminu ya sauya tamkar makoki.

duk wata annashuwa da alfahari da yake alfahari da ita a da, ta shige masa ta barshi da nadama da dimuwa.

Alhaji Saminu ya dinga zubar da hawaye cikin sirri — hawaye na butulci da rashin amana da ya yi wa baffa Moddibbo, wanda ya amince da shi ya ba shi Halima cikin kwanciyar hankali.
yanzu kuma ya gane: ya ci amanar sa... kuma duniya ta rama masa cikin kunya da asara!
zuciyarsa ta kasa kwanciya.
Ko motsin iska da aka yi cikin gida sai ya tuno Halima ,ya zauna ya shafa kansa yana cewa:
"Ni Saminu... ni na kashe Halima da hannu na. ni na lalata amana!"

A ɓangaren Abdullahi kuwa, yana zaune cikin ofishinsa ne duka business da meetings ɗin sa suna tafiya, amma zuciyarsa ta gaza samun natsuwa tun ranar da suka rabu a hotel.

Ana cikin haka sai ya ga sakon gaggawa daga Alhaji Saminu:
"Ina mai baka hakuri, Halima ta tafe gidan gaskiya yanzu ta tafi ta tafe da kuka rashin ka tabbas soyayyar da take ma gaskiya ne ... ta mutu kuma ban cancanci gafararta ba."

Zuciyarsa ta buga!
Idanunsa suka cika da kwalla.
ya dinga kallon sakon kamar zai kira Halima ta amsa masa amma ya sani, babu mai amsawa.

"kin mutu Halima?..." Ya fadi da baki a raunane, numfashinsa yana fita da ƙyar.
sai wayar ta faɗi daga hannunsa.
Gaban mutane sai ya durƙusa.
kamar an fasa masa zuciya, dukkan jikinsa ya rikice, gaba ɗaya duniya ta tsaya masa cikakkar shiru.

"Halima...
Halima...
na bar ki cikin wahala,  na kashe ki da rashin ƙarfin zuciya ta..."

Cikin kukan da bai taɓa fuskanta ba a rayuwarsa, Abdullahi ya fito daga taron ya fice kamar mahaukaci, yana rike kirjin sa da hannuwa biyu, yana kuka tamkar jariri, yana ambaton sunanta.

Duniya ta kare masa a wannan rana.
ya rasa komai.
ya rasa zuciyarsa.
ya rasa Halimarsa
sai tunanin mafarkinsu na yara ya fara dawo masa.
yanda take dariya, yanda take tsoron iska mai kaɗawa...
yanda suka tsaya suna kallon juna a hotel ba tare da sun fahimci komai ba — har abada.
Abdullahi ya narke kamar karamin yaro yana kuka ,ya rasa inda zai kai zuciyarsa.
Soyayyar Halima ta zama masa mafita da karfi.
yanzu kuwa... an binne mafarkin sa da soyayyarsa a ƙasa.

ƘARSHEN LABARIN HALIMA

Bayan rasuwar Halima, kwana biyu kacal sai Abdullahi ya tashi daga gida ya nufi inda aka binne ta , zuciyarsa cike da nauyi kamar dutse mai nauyi, idonsa kuwa har ya kumbura da kuka da rashin bacci.

Lokacin da ya isa makabarta, an waye gari — iska tana kadawa, rana na nufar faduwa.
kabarin Halima yana can gefe, kamar ba halitta ce ciki ba  wsai iska da tsuntsaye.

Abdullahi ya tsaya daga nesa yana kallon kabarin — jikinsa ya mutu, zuciyarsa tana sukar numfashi kamar zai yanke, ya karaso a hankali, kafafunsa kamar an daure su
ya durƙusa a gaban kabarin, ya dafa ƙasa da hannayensa biyu cikin rawar murya ya fara addu'a:
"Ya Allah, ka gafarta wa Halima... Ka sanyata cikin Aljannah tayi ƙoƙari ta zauna da kowa da mutunci ta sha wahala ta mutu cikin rashin adalci. Allah ka mayar mata da jin daɗin da duniya ta hana ta."
"Allah ka haɗa zuciyata da ita a lahira idan babu haduwa a duniya."

Yana cikin addu'a sai hawayensa suka fara gangarowa ba tare da ya lura ba.
Kamar yaro ƙarami ya fashe da kuka mai sauti, yana jijjiga kansa da kafadunsa.
mai karatu da kansa sai ya ji zuciyarsa na karyewa — hawaye na sauka daga idonsa.
Domin kuka ne na gaskiya, na azaba da soyayya da ba ta sami cikar burinta ba.

Abdullahi ya zauna a ƙasa har rana ta fara faduwa.
Iska mai kaɗawa tana motsa ganyen kabari.

Daga nan sai ya ɗaga kansa sama, yana kallon sararin samaniya da idon da ya riga ya ƙumbura, yana faɗin cikin muryar da ta rame:
"Halima... zaki kasance a zuciyata har abada."
"kaddarata ta jefa ni nesa da ke, amma soyayyarki za ta kasance kamar numfashina."
"Allah ya haɗa mu a wuri mafi alheri."

Daga nan ya tashi da ƙyar, yana tafiya daga kabarin da matakin zuciya mai nauyi — ya bar soyayya a ƙasa, ya ɗauki kewa a zuciya.

Maryam ta yi shiru na ɗan lokaci, idanuwanta na cike da hawaye waɗanda suka zuba akai-akai.
Ihsan ta dafa kafadarta cikin tausayawa—tun daga farkon labarin Halima ta kasa dafa kuka.
John, da alama ba zai iya zamewa ba, ya gyada kai da ƙiyayya:
“Maryam, me irin labari ne wannan? mai tsuma zuciya, mai ban tausayi… me yasa ta mutu? me yasa ba su haɗu ba daga kallo na biyu suka rabu?”

Yazid kuma, wanda zuciyarsa ta yi sanyi ganin halin da ƴan masarautarsu suka tsinci kansu, sai ya sauke ajiyar zuciya, ya ce:
“Na yi tunanin zaki ba mu labarin da zai ƙarfafa mana zuciya amma sai gashi kin ba mu labarin da ya tabbatar mana: ba kowane buri ne a duniya zai taɓa cika yadda muke so ba.”

"Ƴan uwa na matafiya "suka kalle juna Gaskiya ce: a duniyar marubuta da ʼyan wasan kwaikwayo, za a samo labarin da ya haɗa auren jarumai har su cika buri amma a zahiri akwai ƙaddara a soyayya—ba duk buri ne ke cika ba. anan sai Maryam ta miƙa ɗan gajeren labari na gaba, na Ummi:
"Ummi maƙobchiyar mu, tun tana yarinya take soyayya da ɗan uwanta. , sun yi rayuwar ƙauna mai ƙarfi ƙaddara bai amince ta aure saba nan ta aure wani daban amma mijinta ya sake ta, ya ci gaba da rayuwarsa ta chigaba da jimammen zawarci duk da haka, soyayyarsu ta ƙarfafa su na shekaru , suka sake ƙulla amana da alkawarin aure …

Amman kash ƙaddara bata amince ba Allah bai yardar musu ba nan aka haramta mata auren sa yanzu ta kuma yin wani aure sun zaɓi ɗaya a zuciyarsu, sun ƙebewa junansu ƙauna ta musamman wannan labarin na gaske ne—ba don jin daɗi ba, amma domin mu gane: soyayya na da ƙaddara, kuma ba koyaushe ake samun ƙarshe mai daɗi ba."
sn kasance cikin shiru da tunani, kowa na jin wannan sabuwar hanyar rayuwa—ta ƙauna da raɗaɗi

BACK TO STORY
zamu chigaba da labarin matafiya guda biyar Maryam ta bamu labarin HALIMATU SADIYA gaskiya ne kaina wannan page ya sani hawaye tabbass soyayya gaskiya ne kuma ba kowane soyayyar bace cikakkiyar.
Ihsan ta bamu labarin Princeces Rahilat
zamu chigaba da tafiya daga Egypt har Dubai ko da ƙafa ne fans ku shirya wannan shine karshen Bayan wata book one

sai mun haɗu a kashi na biyu
********
Alhamdullah
Narnah ƙanwar soja ✍️